YAHUDANCI KIRISTANCI DA MUSULUNCI

JUDAISM CHRISTIANITY AND ISLAM

BLDR. IBRAHIM MUHAMMAD DANKYAURI

HAUSA

ABUBUWAN DA KE CIKI

SHAFI

1 Gabatarwa 3

2 Shinfiɗa 5

3 Asalin Ɗan Adam da Addininsa 5

4 Shaidar Samuwar Ɗan Adam 6

5 Karrama Ɗan Adam, Sauko da shi Duniya da Karƃar Tubansa 8

6 Kasancewar Al'umma ɗaya kan Addini ɗaya tun Asali 10

7 Farkon kaucewar Ɗan Adam daga kan Addini ɗaya ƙwal mai ɗauke da Tsantsar Tauhidi 10

8 Aiko da Shiriya (Addini) ga Ɗan Adam da Aljani 12

9 Halin da ake ciki 15

10 Annabi Musa AS (Moses) 16

11 Annabi Isa AS (Jesus) 30

12 Annabi Muhammad SAW 47

13 Kammalawa 93

1 - GABATARWA

Da sunan Allah Mafi Rahama Mafi Jin ƙai. Dukkan Yabo da Godiya sun tabbata ga Allah Ubangijin kowa da komai. Kuma dukkan Tsarkin da babu wani datti tattare da shi, ya daɗa Tabbata ga Allah SWT. Babu Tsimi babu Dabara sai daga Allah ‘Azza Wa Jalla (AWJ)

Ina daɗa shaidawa babu wani abin bautawa da cancanta sai Allah shi kaɗai wanda ba Shi da abokin tarayya cikin MulkinSa da Ikonsa da ƙaddarawarSa. Ina daɗa shaidawa Annabi Muhammadu SAW bawanSa ne kuma manzonSa ne. Na shaida cewar Annabi Isa bawan Allah ne kuma Manzon Allan ne kuma Ruhi ne daga Allah wanda Ya Jefa cikin mahaifar Nana Maryama har ta haifeshi. Haka na shaida Annabi Musa bawan Allah ne kuma Manzon Allah wanda Allah SWT Ya yiwa Magana ba tare da wasiɗa ba.

Ya Allah, Mai Rahama Mai jin ƙai, Ka ƙara daɗin Tsira da Aminci ga BawanKa kuma ManzonKa Annabin Rahama, Annabi Muhammad SAW, da Iyalan gidansa Tsarkaka da Sahabbansa Adalai da ragowar ManzanninKa da suka gabaceshi da sauran Salihan bayinKa waɗanda ke kan TafarkinKa Madaidaici, Tafarkin waɗanda Ka yi Ni'ima a garesu, ba tafarkin waɗanda Ka yi fushi da su ba, kuma ba tafarkin ɓatattu ba.

Wannan littafi ya ƙunshi darussa cikin irin koyarwar Manyan Manzannin Allah SWT uku na ƙarshen nan, da kuma irin jirkitawar da mabiya Shaiɗanu suka yi galaba ciki domin kawar da Al'umma ga barin Tafarki Madaidaici cikin kowannensu (koyarwar).

Kuma ya ƙunshi ɓangarori goma sha uku kamar yadda suke a cikin shafin abubuwan da ke ciki nan sama kaɗan, amma an dunƙule su kamar haka:

a) Bayan gabartawa da shinfiɗa, daga kan ɓangare na uku (3) Asalin ɗan Adam zuwa na tara (9) Halin da ake ciki, duk bayanai ne na asalin samuwar ɗan Adam a doron ƙasa da turka-turkar fahimtar da shi dalilin da ya sa aka ma halicce shi tun farko, cikin irin Tsarin Bayanan da suka zo cikin Alkurani Mai Tsarki.

b) Daga bangare na goma (10) zuwa na goma sha uku (13), bayanai ne na manyan Annabawan wannan Addini na Musulunci. Kowanne Annabi anyi amfani da Littafinsa wajen kafa hujjar koyarwarsa, da kuma nuna goyon bayansa daga cikin Littafin ƙarshe. Bayanai na irin gurɓatar da wasu maƙiya Allah, suka yi cushe ciki domin kawar da Mutane daga kan Asalin Tafarkin Koyarwar, domin Son zuciya da Iblis ya zamo shine mai yi musu Jagora.

Littattafai da Annabawansu

Manzo / Annabi	Littafinsa	Da Turanci	Larabci
Annabi Musa AS	Tsohon Alƙawari	Old Testament	Attaura
Annabi Isa AS	Sabon Alƙawari	New Testament	Linjila
Annabi Muhammad SAW	Alƙawarin Ƙarshe	Final Testament	Alkur'ani

Bayanan taƙaitattun kalmomi

Taƙaitattu	Bayanai	Fassara
(SWT) ga Allah	Subhanahu Wa Ta'ala	Girman TsarkinSa da ƊaukakarSa
(AWJ) ga Allah	'Azza Wa Jalla	Mabuwayi da Ɗaukaka
(JJ) ga Allah	Jalla Jalalahu	TsarkinSa Ya Ɗaukaka
(SAW) ga Annabi Muhammad	Sallallahu 'Alaihi Wasallama	Allah Ya yi Salati da Sallama Gareshi
(AS) ga ragowar Manzanni	Alaihis Salaam	Aminci a Gareshi
(RA) ga Shahabi daya	Radiyallahu 'Anhu	Allah Ya Yarda da Shi
(RAm) ga Sahabbai da yawa ko biyu	Radiyallahu 'Anhum/ 'Anhumaa	Allah Ya Yarda da Su

2 - SHINFIƊA

Assalin Addinin da Allah SWT Ya ringa saukarwa domin Shiriya ga bayinSa shine Addini mai suna Al-Islam. Kalma ce ta Larabci ma'anarta, Sallamawa, Miƙa Wuya. An ciro ta ne daga asalin kalmar s-l-m (Salam) watau Aminci, Kwanciyar Hankali da Nutsuwa. Watau da Sallamawa ne ko miƙa wuya, ake samun aminci, kwanciyar hankali da nutsuwa.

Sallamawa da miƙa wuya ga wa? Sallamawa da miƙa wuya ga Allah SWT Mahaliccin kowa da komai, cikin ƙaunarSa, biyayya gareShi cikin umarni na yi da hani - SHARI'ARSA - cikin duk Addinan, fatan samun RahamarSa da jin ƙanSa, da kuma tsoron fushinSa da azabarSa. Duk wannan cikin koyarwa, yarda, ƙauna da biyayya ga Manzon da Allah Ya aiko ga jama'ar.

Waƈansu Manzannin sun sami mabiya da yawa, wasu kuma kaƈan, kai wasu mutun ƈaya ko biyu suka samu, wasu babu mutun ko ƈaya da ya bisu ya yarda da kiransu, duk da sun isar da saƙon Allah SWT.

Farkon abinda kowanne Manzo ya yi kira ga al'umma shine a bautawa Allah Shi kaƈai ba tare da an yi shirka da Shi ba. Sannan sai koyar da ilimi tare da hujjoji na sanin Allah. Sai kuma ragowar Ibada (ta gaƃoƃi da zuciya) da mu'amalar zamantakewa tsakanin ƴan Adam domin kwanciyar hankalinsu, jin dadin su da ci gaban rayuwarsu a dunƙule.

3 - ASALIN ƊAN ADAM DA ADDININSA.

Ɗan Adam halittace da Allah SWT Ya halitta da HannayenSa biyu tun Asali. Maganar Darwin ko aƙidar Darwism ƙarya ce ƙerarriya, marras asali cikin dukkan Addinan da aka saukar daga sama. Ba wai wata halittace ta daban a cikin ruwa ba, wadda ta rikiƈe ta zama ƈan Adam ta dawo kan tudu ta bar cikin teku. Halittun ruwa da ban suke da na kan tudu. Na kan tudunma sun rarrabu,

akwai masu tafiya kan ƙafofi biyu, wasu kan ƙafofi huɗu, wasu masu jan ciki, wasu masu tashi sama. Kowanne an hore masa inda zai rayu har zuwa mutuwarsa abar ƙaiyadewa.

Tun Asali haka Allah Ya halicce shi kuma yake nan haka har yanzu. Kamar yadda saniya, tattabara, sauro, ƙadangare, da bishiyar ayaba, lemo, inibi, suke tun Asalin halittarsu ta farko, to har yau ɗinnan haka suke. Canjin kawai shine na girman jiki. Abinda yake ya sami abinci da lafiya, yayi jibgege ƙato da kyan jikin, abinda bai sami abinci lafiyayye ba, ga kuma cuta ya motse. Amma dai shine tun asalinsa. Shi ya sanya, Allah cikin HikimarSa Ya ƙaddara aure, jima'i, ɗaukar ciki, haihuwa da raino, domin kiyaye halittar Asalin. Kuma haka abin yake ga tsirrai da ragowar dabbobi na ruwa da kan tudu. Yana ɗaya daga cikin dalilai domin kiyaye halittar Asali, doka cikin Addinin Musulunci cewar duk wanda ya yi jima'i da dabba, a kashe dabbar tare da shi. Haka dan luwaɗi da 'yar maɗugo duk a yi musu mummunan kisa, da wanda yake yi da wanda ake yiwa. Canza Halitta mummunan zunubi ne a Addinin Musulunci. Allah Ne Mafi sani.

4 - SHAIDAR SAMUWAR ƊAN ADAM.

و إذ قال ربك للملائكة إني جاعل في الأرض خليفة قالوا أتجعل فيها من يفسد فيها و يسفك الدماء و نحن نسبح بحمدك و نقدس لك قال إني أعلم ما لا تعلمون

Kuma a lõkacin da Ubangijinka Ya ce ga malã'iku: "Lalle ne, Ni Mai sanya wani halĩfa ne a cikin ƙasa," suka ce: "Ashe, zã Ka sanya a cikinta, wanda zai yi ɓarna a cikinta, kuma mu, muna yi maka tasbihi tare da gõde maka, kuma muna tsarkakewa gareka" Ya ce: "Lalle ne, Ni Na san abin da ba ku sani ba." Surah Al-Baqarah aya ta 30.

إذ قال ربك للملائكة إني خالق بشرا من طين

A lõkacin da Ubangijinka Ya ce wa malã'iku, "Lalle Nĩ Mai halitta mutum ne daga lãkã. Surah Ṣād aya ta 71.

الذي أحسن كل شيء خلقه و بدأ خلق الإنسان من طين

ثم جعل نسله من سلالة من ماء مهين

ثم سواه و نفخ فيه من روحه و جعل لكم السمع و الأبصار و الأفـءدة قليلا ما تشكرون

و قالوا أءذا ضللنا في الأرض أءنا لفي خلق جديد بل هم بلقاء ربهم كافرون

قل يتوفاكم ملك الموت الذي وكل بكم ثم إلى ربكم ترجعون

Wanda Ya kyautata kõme, Wanda Ya halitta shi. Shi ne kuma Ya fãra halittar mutum daga lãka.

Sa'an nan Ya sanya ɗiyansa daga wani asali na wani ruwa wulãkantacce.

Sa'an nan Ya daidaita shi, kuma Ya hũra a cikinsa, daga ruhinSa kuma Ya sanya muku ji, da ganunuwa da zukãta. Gõdiyarku kaɗan ce ƙwarai.

Kuma suka ce: "Shin, idan mun ɓace a cikin ƙasã (mun rududduge mun zama ƙasa), shin, lalle mu, tabbas ne munã zama a cikin wata halitta sãbuwa?" Ã'a, su game da gamuwa da Ubangijinsu kãfirai ne.

Ka ce: "Mala'ikan mutuwa ne. wanda aka wakkala a gare ku, shĩ ne ke karɓar rãyukanku. Sa'an nan zuwa ga Ubangijinku ake mayar da ku." Surah As-Sajdah aya ta 7 zuwa ta 11.

و لقد خلقنا الإنسان من سلالة من طين

ثم جعلناه نطفة في قرار مكين

ثم خلقنا النطفة علقة فخلقنا العلقة مضغة فخلقنا المضغة عظاما فكسونا العظام لحما ثم أنشأناه خاقا ءاخر فتبارك الله أحسن الخالقين

ثم إنكم بعد ذالك لميتون

ثم إنكم يوم القيامة لتبعثون

Kuma lalle ne, haƙĩƙa, Mun halitta mutum daga wani tsantsa daga lãka.

Sa'an nan kuma Muka sanya shi, ɗigon maniyyi a cikin matabbata natsattsiya.

Sa'an nan kuma Muka halitta shi gudan jini, sa'an nan Muka halitta gudan jinin tsõka, sa'an nan Muka halitta tsõkar ta zama ƙasũsuwa, sa'an nan Muka tufãtar da ƙasũsuwan da wani nãma sa'an nan kuma Muka ƙãga shi wata halitta dabam. Sabõda haka albarkun Allah sun bayyana, Shi ne Mafi kyawun mãsu halittawa.

Sa'an nan kuma ku, bãyan wannan, lalle ne masu mutuwa ne.

Sa'an nan kuma lalle ne kũ a Rãnar alkiyãma, za a tãyar da ku," Surah Al-Muʾminūn aya ta 12 zuwa ta 16.

سبحان الذي خلق الأزواج كلها مما تنبت الأرض و من أنفسهم و مما لا يعلمون

Tsarki ya tabbata ga Wanda Ya halitta nau'uka, namiji da mace, dukansu, daga abin da ƙasã ke tsirarwa, kuma daga kansu, kuma daga abin da basu sani ba. Surah Ya-Sin aya ta 36.

5 - KARRAMA ƊAN ADAM, SAUKO DA SHI DUNIYA DA KARƁAR TUBARSA.

و إذ قلنا للملائكة اسجدوا لآدم فسجدوا إلا إبليس أبى و استكبر و كان من الكافرين

و قلنا يآ ءادم اسكن أنت و زوجك الجنة و كلا منها رغدا حيث شءتما و لا تقربا هذه الشجرة فتكونا من الظالمين

فأزلهما الشيطان عنها فأخرجهما مما كانا فيه و قلنا اهبطوا بعضكم لبعض عدو و لكم في الأرض مستقر و متاع إلى حين

فتلقى ءادم من ربه كلمات فتاب عليه إنه هو التواب الرحيم

قلنا اهبطوا منها جميعا فإما يأتينكم مني هدى فمن تبع هداى فلا خوف عليهم و لا هم يحزنون

Kuma a lõkacin da Muka ce ga malã'iku: "Ku yi sujada ga Ãdam," Sai suka yi sujada, fãce Ibilĩsa ya ƙi, kuma ya yi girman kai, kuma ya kasance daga kãfirai.

Kuma muka ce: "Ya Ãdam! Ka zauna kai da matarka a gidan Aljanna, kuma ku ci daga gare ta, bisa wadãta, inda kuke so, kuma kada ku kusanci wannan itãciyar, har ku kasance daga azzãlumai."

Sai Shaiɗan ya talãlãƀantar da su ga barinta, sai ya fitar da su daga abinda suka kasance a cikinsa. Kuma Muka ce: "Sãshenku nã maƙiyi ga sãshe, kuma kuna da a cikin ƙasa matabbata da jin dãɗi zuwa ga wani lõkaci."

Sai Ãdam ya karƀi wasu kalmõmi daga Ubangjjinsa, sabõda haka Ya karƀi tũba a kansa. Lalle ne Shi, Shĩ ne Mai karƀar tũba, Mai jin ƙai.

Muka ce: "Ku ku sauka daga gare ta gabã ɗaya. To, imma lalle shiriya ta je muku daga gare Ni, to, wanda ya bi shiriya ta to, bãbu tsõro a kansu, kuma bã su yin baƙin ciki." Surah Al-Baqarah aya ta 34 zuwa 38.

و لقد كرمنا بني ءادم و حملناهم في البر و البحر و رزقناهم من الطيبات و فضلناهم على كثير ممن خلقنا تفضتلا

Kuma lalle ne Mun girmama 'yan Adam, kuma Muka ɗauke su a cikin ƙasa da tẽku kuma Muka azurta su daga abũbuwa mãsu dãɗi kuma Muka fĩfĩta su a kan mãsu yawa daga waɗanda Muka halitta, fĩfĩtãwa." Surah Al-Isra'i aya ta 70.

6 - KASANCEWAR AL'UMMA ƊAYA KAN ADDINI ƊAYA TUN ASALI.

وما كان الناس إلا أمة واحدة فاختلفوا ولولا كلمة سبقت من ربك لقضي بينهم فيما فيه يختلفون

"Kuma mutãne ba su kasance ba fãce Al'umma guda (kan Addini guda ɗaya Tilo), sa'an nan kuma suka sãƀãwa jũna, kuma ba dõmin wata kalma ba wadda ta gabãta daga Ubangijinka, dã anyi hukunci a tsakãninsu a kan abinda yake a cikinsa wadda suka sãƀãwa jũna." Surah Yunus aya ta 19.

كان الناس أمة واحدة فبعث الله النبيين مبشرين و منذرين و أنزل معهم الكتاب بالحق ليحكم بين الناس فيما اختلفوا فيه وما اختلف فيه إلا الذين أوتوه من بعد ما جاءتهم البينات بغيا بينهم فهدى الله الذين ءامنوا لما اختلفوا فيه من الحق بإذنه والله يهدي من يشاء إلى صراط مستقيم

"Mutãne sun kasance al'umma guda ɗaya. (Da suka rarrabu) Sai Allah Ya aiki annabãwa suna mãsu bãyar da bishãra kuma mãsu gargaɗi; kuma Ya saukar da Littãfi da gaskiya tãre da su dõmin (Littãfin) ya yi hukunci a tsakãnin mutãnen a cikin abinda suka sãƀãwa jũna a cikinsa. kuma bãbu wanda ya sãƀã, a cikinsa, fãce waɗanda aka baiwa shi daga bãyan hujjõji bayyanannu sun je musu dõmin zãlunci a tsakãninsu. Sai Allah Ya shiryar da waɗanda suka yi ĩmani ga abinda suka sãƀã a cikinsa daga gaskiya da izninSa. Kuma Allah Yana shiryar da wanda Yake so, zuwa ga hanya madaidaiciya." Surah Al-Baqarah aya ta 213

7 - FARKON KAUCEWAR ƊAN ADAM DAGA KAN ADDINI Ɗ AYA ƘWAL MAI ƊAUKE DA TSANTSAR TAUHIDI.

Koda yake asalin Dan Adam akan Tauhidi yake tun farkon halittarsa, to me ya haifar da kaucewarsa har Allah SWT Ya fara aiko da Manzanni?

Kamar yadda muka karanta nan baya cewar Allah SWT Ya fitar da Annabi Adamu Alaihis Salaam (AS) da matarsa Hauwa'u daga Aljanna zuwa Duniya tare da Iblis watau Shaiɗan, cewa dai duk wanda yabi ShiriyarSa ta hanyar Manzanni ya kuƃuta daga sharrin Shaiɗan. Sai ya kasance duk rãyuwar Annabi Adamu kafin ya rasu a nan Duniya tare da 'ya'yansa suna kan Tauhidi tsantsa kamar yadda Allah SWT Ya umarcesu. Annabi Adamu ya rayu shekara ɗari tara da sittin sannan tsakaninsa da farkon Manzon da aka fara aikowa ga 'ya'yansa watau Annabi Nuhu AS, ƙarni goma ne watau shekara dubu. A cikin wannan shekaru dubun, bayan rasuwar Annabi Adamu, 'ya'yansa suka jirkita Addinin gaskiya mai ɗauke da Tsantsar Tauhidi suka koma bautawa gumaka da Shehunnai.

Yadda abin yake shine; daga cikin 'ya'yan Annabi Adamu akwai manyan masu tsoron Allah tare da kyautatawa da yawan bautarsu ga Allah SWT. Sunayen wasunsu akwai kamar haka; Wadda, Suwa'a, Yagusa, Ya'uƙa da Nasra.

Bayan iri-irin waɗannan manyan Shehunnai (Wadda da Suwa'a da sauransu) sun rasu, sai ilimin Addinin bautawa Allah Shi kaɗai (Tauhidi) yayi rauni. Bayan wasu ƙarnoni daga cikin ƙarni goman can (kafin aiko Annabi Nuhu), sai Jama'a suka fara shauƙin waɗancan manyan malamai da suka rasu (ta hanyar karanta tarihinsu). Daga nan sai Iblis ya riya musu cewar mai zai sa ba za su yi mutun-mutuminsu ba domin ko yaushe suka ga gumakansu sai su tuna dasu sannan hankalinsu ya kwanta? Suka karƃi shawarar Iblis. Bayan waɗanda suka yi gumakan waɗancan Shehunnai sun rasu sai Iblis ya sake ziyartar na bayansu ya ce musu; "kun ga waɗannan gumakanfa da kuke gani a guraren Ibadarku, mutanen da suka gabaceku (kakannin kakanninku) bauta musu suke yi. Shikenan sai bautar Allah ta shuɗe, aka koma bautawa gumaka. Saboda Rahamar Allah ga 'ya'yan Adamu, bai barsu haka kan Shirka da kafirci ba, sai Ya aiko musu da Manzon Farko Annabi Nuhu AS domin komawa ga Addini ɗ aya na Tauhidi.

Lokacin da Annabi Nuhu AS yake ta wa'azi domin komawa ga Tauhidi, shin duk Jama'arsa sun karbi kiransa domin koma kan Addini ɗaya ƙwal? A'a sai yan ka ɗan. Shi ya sanya Allah Ya umarce shi da sassaka jirgin ruwa wadda zai dauke shi da ragowar waɗanda suka yi Imani da abinda aka aiko musu na Tauhidi da sauran dabbobi nau'i bibbiyu. Sannan Ya aiko da ruwan ɗufana wanda ya halakar da kangararru kuma Ya tseratar da Annabi Nuhu da mutanen da suka yi Imani da shi ta hanyar babban jirgin ruwan da ya ɗebesu.
Mu sani Iblis ɗan tawaye shugaban mahassada da kangararru, kuma maƙiyin banu Adama yana nan har yau, kuma yayi Alƙawarin halakar da 'yan Adam. Wannan kuwa a baiyane yake ta yadda har yau akwai masu bautawa Shehunnai da hotunansu a cikin Al'ummar Musulmai a wannan ƙasa tamu.

Abin farin cikin shine, Allah Mai Rahama da Gafara ga bayinSa Yana nan, Shi kuma har bayan gobe, sannan Yayi Alƙawarin kare bayinSa na gari daga Sharrin Shaiɗan. Shi yasa har kullum sai an sami masu kare Tauhidi, in sha Allah.

8 - AIKO DA SHIRIYA (ADDINI) GA ƊAN ADAM DA ALJAN.

{ وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن رَّسُولٍ إِلَّا بِلِسَانِ قَوۡمِهِۦ لِيُبَيِّنَ لَهُمۡۖ فَيُضِلُّ ٱللَّهُ مَن يَشَآءُ وَيَهۡدِي مَن يَشَآءُۚ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ }

Kuma ba Mu aika wani Manzo ba fãce da harshen mutãnensa dõmin ya bayyanã musu. Sa'an nan Allah Ya ƙatar da wanda Yake so kuma Ya shiryar da wanda Yake so, Kuma shĩ ne Mabuwãyi, Mai hikima. [Surah Ibrāhīm: 4]

شرع لكم من الدين ما وصى به نوحا و الذي أوحينا إليك و ما وصينا به إبراهيم و موسى و عيسى أن أقيموا الدين و لا تتفرقوا فيه كبر على المشركين ما تدعوهم إليه الله يجتبى إليه من يشاء و يهدى إليه من ينيب

"Ya shar'anta muku, game da addini, abinda Ya yi wasiyya da shi ga Nũhu (Noah) da abinda Muka yi wahayi da shi zuwa gare ka (Ya Muhammad), da abinda Muka yi wasiyya da shi ga Ibrãhĩm (Abraham) da Mũsã (Moses) da Ĩsã (Jesus), cẽwa ku tsayar da addini sõsai kuma kada ku rarrabu a cikinsa. Abinda kuke kira zuwa gare shi (cewa a bautawa Allah ɗaya Tilo) ya yi nauyi a kan mãsu shirki. Allah na zãƀen wanda Yake so zuwa gare Shi, kuma Yanã shiryar da wanda ke tawakkali gare Shi, ga hanyarSa." Suratu Ash-Shura aya ta 13.

الم

تنزيل الكتاب لا ريب فيه من رب العالمين

أم يقولون افتراه بل هو الحق من ربك لتنذر قوما ما اتاهم من نذير من قبلك لعلهم يهتدون

Alif, Lām, Meem.

Saukar da Littafin bãbu shakka a gare shi, daga Ubangijin tãlikai yake.

Kõ sunã cẽwa (Muhammadu ne) ya ƙirƙira shi? Ã'a, shĩ ne gaskiya daga Ubangijinka, dõmin ka yi gargaɗi ga mutãne waɗanda wani mai gargaɗi bai je musu ba a gabãninka, fãtan zã su shiryu. Surah As-Sajdah ta 1 zuwa ta 3.

و ما أرسلنا من قبلك من رسول إلا نوحي إليه أنه لا إله إلا أنا فأعبدون

Kuma ba Mu aiki wani Manzo ba a gabãninka fãce Munã yin wahayi zuwa gare shi, cẽwa "Lalle ne Shi, bãbu abin bautãwa fãce Ni (Allah), sai ku bauta Mini." Surah Al-Anbiya aya ta 25.

و لقد أنزلنا إليكم ءايات مبينات و مثلا من الذين خلوا من قبلكم و موعظة للمتقين

Kuma lalle ne Mun saukar zuwa gare ku, ãyõyi mãsu bayyanãwa, da misãli daga waɗanda suka shige daga gabãninku, da wa'azi ga mãsu taƙawa. Surah An-Nur aya ta 34.

الذين ءامنوا و لم يلبسوا إيمانهم بظلم أولاءك لهم الأمن و هم مهتدون

"Waɗanda suka yi ĩmãni, kuma ba su gauraya ĩmãninsu da zãlunci ba, waɗannan sunã da aminci, kuma sũ ne shiryayyu." Surah Al-Anʿām aya ta 82.

و وصى بها إبراهيم بنيه و يعقوب يا بني إن الله اصطفى لكم الدين فلا تموتن إلا و أنتم مسلمون

أم كنتم شهداء إذ حضر يعقوب الموت إذ قال لبنيه ما تعبدون من بعدي قالوا نعبد إلاهك و إله ءاباءك إبراهيم و إسماعيل و إسحاق إلها واحدا و نحن له مسلمون

تلك أمة قد خلت لها ما كسبت و لكم ما كسبتم و لا تسألون عما كانوا يعملون

"Kuma Ibrãhĩm(Abraham) ya yi wasiyya da ita ga ɗiyansa, kuma Ya'aƙũbu (Jacob) (ya yi wasiyya, suka ce:) "Yã ɗiyãna! Lalle ne, Allah Ya zãɓã muku addini don haka kada ku mutu, lalle, fãce kuna Musulmi."

"Ko kun kasance halarce a lõkacin da mutuwa ta halarci Ya'aƙũbu (Jacob), a lõkacin da ya ce wa ɗiyansa: "Mẽne ne zã ku bautawa daga bãyãna (idan na rasu)?" Suka ce: "Muna bautawa Abin bautawarka kuma Abin bautawar ubanninka Ibrãhĩm (Abraham) da Ismã'ĩla (Ishmael) da Is'hãƙa (Isaac), Ubangiji Guda, kuma mu a gare Shi mãsu miƙa wuya ne."

"Waccan, wata al'umma ce, ta riga ta shige, tana da abin da ta sanã'anta kuma kuna da abin da kuka sanã'anta, Kuma bã zã a tambaye ku ba daga abinda suka kasance suna aikatãwa." Surah Al-Baqarah aya ta 132 zuwa ta 134.

Kamar yadda muka gani cikin abinda ya gabata ne cewar an fara aiko Manzanni ne, bayan jama'a sun fara rarrabuwa suna zama ƙungiya-ƙungiya ta ɓata daga kan tafarkin TAUHIDI. Annabi Noah AS ne farkon Manzo.

9 - HALIN DA AKE CIKI

Haka abin ya kasance, duk lokacin da tafiya ta yi nisa sai Iblis ya rikirkitar da yayan Adam daga barin Addinsu na Asali. Amma Allah cikin RahamarSa sai Ya aiko da sabon Manzo domin mayar da mutane kan Asalin.

Yanzu zamu ɗauki kowanne ɗaya daga cikin Addinin Manzanni ukun ƙarshe - Annabi Musa, Annabi Isa da Annabi Muhammad SAW, muga irin Koyarwarsu, da kuma irin yadda Iblis yake kai komo ciki domin sake rikirkitar da jama'a, a da can da yanzu.

Kafin nan ga jerin sunayen Annabawa da Manzanni da suka zo cikin Alƙur'ani da Linjila (The Bible) da Attaura (The Torah), tun daga kan Adam uban kowa. Waɗannan sune waɗanda Allah SWT Ya bayar da labarin su cikin LittattafanSa, amma yawansu yafi haka kamar yadda Ya ce "babu wata al'umma face an aika mata da mai gargaɗi".

SUNAYEN ANNABAWA

Alƙur'ani ya ambaci guda ashirin da biyar kamar haka:

1. Adam 2) آدم(. Idris (إدريس) (Enoch) 3. Nuh (نوح) (Noah) 4. Hud (هود) (Eber) 5. Saleh 6) صالح(. Ibrahim (إبراهيم)(Abraham) 7. Lut (لوط) (Lot) 8. Ismail (إسماعيل) (Ishmael) 9. Ishaq (إسحاق) (Isaac) 10. Ya'qub (يعقوب) (Jacob) 11. Yusuf (يوسف) (Joseph) 12. Ayub (أيوب) (Job) 13. Shu'aib (شعيب) (Jethro) 14. Musa (موسى) (Moses) 15. Harun (هارون) (Aaron) 16. Dul-Kifl (ذو الكف) (Ezekiel) 17. Dawud (داود) (David) 18. Sulaiman (سليمان) (Solomon) 19. Ilyas (إلياس) (Elijah) 20. Al-Yasa (اليسع) (Elisha) 21. Yunus (يونس) (Jonah) 22. Zakaria (زكريا) (Zechariah) 23. Yahya (يحيى) (John the Baptist) 24. Isa (عيسى) (Jesus) 25. Muhammad (محمد)

10 - ANNABI MUSA (MOSES) AS.

Allah SWT Ya aiko Annabi Musa ga Bani Isra'ila waɗanda a yau ake kira Yahudawa. Yaren ƙabilarsu shine Hibru. Saboda Annabi Musa an aiko shine ga Yahudawa kawai, shi yasa a yau, waɗanda suke cikin ƙabilar Yahudu ne kawai ƁangarenMahaifiyar su, ke da'awar sune mabiya Annabi Musa na asali. Watau sai idan mahaifiyarsa ce kawai Bayahudiya, shine yake Bayahude mai bin Addinin Annabi Musa, koda mahaifinsa ba Bayahude ba ne.

Amma wasu cikinsu sun yarda da cewa, a'a har mahaifinsa. Akwai waɗanda cikin su suka yarda da kasancewar mutum Bayahude idan har ya karɓi Addinin Yahudanci. A dunƙule Addini ne na ƙabilanci shi yasa Yahudawa suke ɣan tsiraru a yau, idan an kwatanta yawansu da ragowar mabiya wasu Addinan.

Har wayau, Addinin Yahudanci ya kasu a ƙalla kaso biyu, - Yahudawa masu riƙo da koyarwar Annabi Musa tsantsa da Yahudawa ɣan "Secularism" waɗanda ba suyi riƙo da dukkannin koyarwar ba, sai ɗan abinda ba a rasa ba. Kuma waɗannan, su suka fi yawa cikin Yahudawa a yau.

A yau shiga Addinin Yahudanci na da Sharuɗa kamar yadda ya zo cikin dokokinsu na Talmud wanda ya samo asali daga dokokin da aka baiwa Annabi Musa.

Na farko: a yiwa mutum kaciya idan namijine. Idan kuma yana da kaciyarsa tuni, to sai a ƙwarzaneta yadda za ta ɗan kwararar da jini.

Na biyu: tsunduma cikin ruwan da aka shar'anta gaban masu shaidawa.

Na uku: ƙudurewa da yarda da Dokoki Goma "The Ten Commandments". Za a yi bayaninsu in sha Allah nan gaba.

An ambaci sunan Annabi Musa da lafazin Musa a cikin Alƙur'ani sau ɗari da talatin da ɗaya (131), Annabi Isa sau ashirin da biyar (25), Annabi Muhammad sau huɗu (4). An ambaci Nana Maryam mahaifiyar Annabi Isa AS sau talatin da ɗaya (31), amma ba a ambaci sunan Mahaifiyar wanda aka baiwa Alƙur'anin ko sau ɗaya ba. Wannan ya nuna cewar Annabi Musa ya sha gwagwarmaya a Duniya. Kuma wannan shi zai daɗa tabbatar maka da adalcin Alƙur'ani da gaskiyarsa, cewa daga Allah SWT yake.

Kamar yadda muka sani cewar bayan Annabi Adamu ya rasu, ɣayan sa sun ci gaba da bautar Allah kan Tauhidi har zuwa lokacin da Tauhidin ya kuɓuce, shine Allah SWT cikin RahamarSa Ya fara turo Annabi Nuhu (Noah) AS domin komawa ga Tauhidi. Abin haka ya taho. Wani lokacin al'umma tana kan Tauhidi, wani lokacin tana kan Shirka, har zuwa lokacin Annabi Musa AS.

Annabi Musa bawan Allah ne na gari wanda Allah SWT Ya zaɓa da Annabta da Manzanci, domin ƙaunar da Allah SWT Yake masa. Allah Ya ba shi Littafin Attaura wadda a cikinta akwai Shiriya da Shari'a bayyananniya. Annabi Musa da ɗan uwansa Annabi Haruna (Aaron) an aiko su ne ga Banu Israel kawai. Shi ya sanya Addinin Yahudanci yake na wani ɓangare ne na Al'umma kawai. A yau idan baka da jinin Yahudu a gareka to ko kana da'awar Yahudanci, su Yahudun na asalin suna ɗaukar ka ne kawai jabun Bayahude.

Annabi Musa ya sha wahala cikin kiran Banu Israela domin su yi Imani da shi. Haka bayan sunyi Imani da shi suka ringa wahalar da shi. Duk da haka a matsayinsa na Manzo ya jure kuma ya kai su ga tafarkin Tsira.

Tarihi ya nuna cewar Banu Israela sun taɓa zama ƙarƙashin mulkin Fir'auna na Masar wanda ya mayar da su tamkar bayi. A cikin wannan hali ne aka haifi Annabi Musa AS a wannan ƙasa ta Masar. Kwatsam sai wani ɗan duba ya faɗawa Fir'auna cewar za a haifi ɗa cikin Banu Israela wanda zai karɓe mulkin Fir'auna. Shike nan sai Fir'auna ya yarda da abinda boka ya faɗa masa. Dalilin

haka yasa duk ɗan da aka haifa na daga Bani Israela a daidai wannan lokacin, sai Fir'auna ya sa a kashe shi. Idan mace aka haifa sai ya barta. To amma suna makirci, Allah Yana mayar musu da makirci. Kuma Allah Shine mafi kyawun masu mayar da makirci. Annabi Musa ya tashi cikin gidan Fir'auna kuma ya raine shi har zuwa lokacin da aka ba shi annabta.

Saboda mutanen Fir'auna sun ƙware cikin tsafi da surkulle, sai Allah SWT Ya baiwa Annabi Musa Mu'ujizozi da suka sha gaban matsafan Fir'auna. Sannan Allah Ya ba shi Attaura mai ƙunshe da Manyan Dokoki Goma cikin Allo, da sauran ragowar ƙa'idojin Shari'ar Banu Israela.

Annabi Musa da jama'arsa sun ɗanɗana kuɗarsu a hannun Fir'auna a Masar. Don haka sukayi Hijira (Exodus) zuwa ƙasarsu ta asali, bayan Allah Ya tseratar dasu daga Fir'auna wanda Ya halakar cikin kogi (kogin Nilu). Saboda kuma saɓawa Annabi Musa da mabiyansa suka ringa yi, Allah Ya barsu cikin ɗimuya da yawo cikin dazuzzuka ta yadda suka ringa kai komo har tsahon shekara arba'in. Saboda wannan ɗimuwar, koyarwar Annabi Musa ta fara rauni cikin zukatan mabiya har suka fara manta wani abu daga ciki. Bayan Annabi Musa ya rasu, almajiransa watau sahabbansa sunci gaba da ɗaukar nauyin Koyarwarsa. Sai dai kash, yaƙoƙi da rusa Jerusalem yasa da yawa daga cikin koyarwar Annabi Musa ta kuɓuce (wadda aka haddace da wadda take a rubuce). Bayan wani lokaci, manyan Malaman Yahudawa na baya baya kamar su Uzair (400 BCE), suka sake harhaɗa koyarwarsa wadda ta kawo har yanzu amma mai kurakurai ciki.

ME ATTAURA TA ƙUNSA A YAU?

Daga abinda ya kasance yanzu cikin Attaurah (TORAH) akwai ƃangarori biyar kamar haka:

i) Farawa, Genesis, ii) Fitowa, Exodus iii) Shari'a, Leviticus iv) Taro, Numbers, v) Khuɗuba, Deuteronomy.

Kowanne ƃangare cikin biyar ɗin nan, yana da surori (chapters) da kuma ayoyi (verses).

i) Farawa, Genesis tana da surori (Chapters) 50

ii) Fitowa, Exodus surori 40

iii) Shari"a, Leviticus surori 27

iv) Taro, Numbers surori 36

v) Khuɗuba, Deuteronomy surori 34

Jumlar Surori 187 (Chapters) a cikin Attaurah. Alƙur'ani yana da Surori 114 (Chapters)

Waɗancan su suka tattara suka zama Attaura wadda Ƴan Mishan suke kira Tsohon Alkawari, "Old Testament". Wanda aka haɗe cikin Littafin Linjila, Littafin Annabi Isa AS mai suna Sabon Alkawari "New Testament". Domin dai su Kiristoci sun yi amanna da Annabi Musa. Shi yasa suka yi majar Littattafan biyu, saƃanin Alƙur'ani "The Final Testament" wanda ya tsaya da ƙafarsa shi kaɗai domin gyara duk abinda yake gurƃattacce na daga Littatafan da suka gabace shi.

Taƙaitaccen bayani kan kowanne ƃangare cikin ƃangarori biyar da suka gabata na Attaura.

i) Farawa (Farkon Halitta, Farkon Ƙarni) da Turanci - **Genesis**.

Ciki Allah Ya bayar da Labarin halittar sammai da ƙasa da abinda ke cikinsu, cewar Shi kaɗai Ya haliccesu (Tauhidur Rububiyya). Ya bayar da labarin Annabi Adam da Hauwa'u (Eve), da labarin yayansu Ƙabil (Cain) da Habil (Abel) da labarin gajiyawar ɗan Adam da sauransu, da kuma tarihin Addininsu (Tauhidul Uluhiyya) na bautawa Allah Shi ɗaya Tilo. Haka tarihin Annabi Nuhu (Noah) farkon Manzanni, da ruwan ɗufana (The Flood). Ya bayar da tarihin Annabi Luɗ (Lot) da ɗan uwansa Annabi Ibrahim (Abraham) da yayansa Annabi Isma'il (Ishmael) da Annabi Ishaq (Isaaq), da tarihin jikan Annabi Ibrahim watau Annabi Ya'aƙub (Jacob) da yayansa Annabi Yusuf (Joseph) da yan uwansa su Binyaminu (Benjamin). Duk wannan za ka same shi cikin Alƙur'ani da cikakken bayani tsararre mafi inganci.

ii) Fitowa (Hijrah) da Turanci - **Exodus**

Cikin wannan ɓangaren akwai labarin yin ƙaurar da Annabi Musa yayi da jama'arsa. Sun fita daga garin Fir'auna inda ake ɗanɗana musu azaba zuwa ƙasar Sham. Akan hanyar tafiya, bayan sun kai zuwa dutsen Sinai (ɗur Sinin) sai Allah Ya baiwa Annabi Musa Dokoki Goma (the Ten Commandments) da ragowar Shari'o'i kuma Ya yi magana da shi.

iii) Dokoki. Shari'ar Yahudu. Da Turanci **Leviticus**

Wannan ɓangaren ya ƙunshi ƙa'idoji na Addinin Yahudanci. Tun daga kan yadda za su yi amfani da ginannun gurin ibadarsu zuwa abinda aka halatta da haramtawa da dokokin yanka da dabbobin da aka halatta da waɗanda aka haramta. Bayanan ranar biki da Shari'o'i kan halaiyar zamantakewa da kuma tsokaci da gwaggwaɓan ladan da mutum zai samu daga Allah idan ya bi kuma ya kiyaye dokokin Allah. Haka tsoratarwa da azaba mai tsanani ga duk wanda ya saɓawa dokokin Allah AWJ. Duba Leviticus 10:8, haramcin shan giya da

ragowar kayan maye. Sai dai kuma wannan ya ci karo da Deuteronomy 15:3,26. Manyan Dokoki goma na cikin Attaura su ne

DOKOKI GOMA (THE TEN COMMANDEMENTS)

1) Ni ne Ubangiji Allahn ku, kada ku riƙi wani abin bauta baicin Ni

2) Kada ku riƙi Sunan Ubangijin ku da isgilanci a wulaƙance

3) Ku tuna tsarkake Ranar Ubangijinku. (Asabar)

4) Ku riƙi mahaifanku abubuwan girmamawa (da ɗaukakawa)

5) Kada ku yi kisan kai

6) Kada ku yi zinace zinace

7) Kada ku yi sata

8) kada ku yi shaidar zur ga maƙwabcinku

9) Kada ku nemi matar maƙwabcinku da lalata

10) Kada ku handime dukiyar maƙwabcinku (bisa zalunci)

iv) Taro (Yawan Sahabban Annabi Musa) da Turanci **Numbers**.

Wannan ƃangaren ya ƙunshi bayanan yawan jama'ar da suka fita tare da Annabi Musa domin zuwa karƃar ƙasar da Allah Ya yi musu alƙawari cewa a can ne za su hayayyafa su yaɗu su zama masu tarin yawa (al'umma ko Nation). Da labarin bijirewar da mutanen Annabi Musa suka yi masa har Allah Ya halakar da yawa daga cikinsu. Har sai da suka jira shekaru masu yawa kafin yawansu da ƙarfinsu ya dawo, sannan suka ci gaba da tafiya zuwa ga wannan ƙasar da aka yi musu alƙawari.

v) Khuɗuba. Ta bin Allah sau da ƙafa da Turanci **Deuteronomy**

Wannan ƃangaren ya ƙunshi khuɗubobi da Annabi Musa ya yi ga jama'arsa kaɗan kafin shiga ƙasar da akayi musu alƙawari. Daga farko, khuɗubar ta ƙunshi bayanai kan irin masifar da suka shiga wadda ta haifar musu da halin da suke ciki, dalilin saƃawa dokokin Allah. Sai tsokaci da bin dokokin Allah sau da ƙafa domin gujewa abkawa cikin irin wannan halin na bala'in fatara da yunwa da cutuka. Sai kuma bayanai kan danƙawa Annabi Yusha'u ragamar kulawa da jama'arsa, daga nan sai bayanin rasuwarsa Annabi Musa AS, bayan shekaru sama da ɗari da ashirin da haihuwarsa. Duba Deuteronomy 14:8, haramcin cin naman Alade da tsuntsaye masu farauta.

Babban abin tsokaci anan shine, yadda Annabi Musa ya koyar da jama'arsa Tauhidin Rububiyya da Uluhiyya da Sifaat cikin Farawa - GENESIS da kuma Hijira - EXODUS.

Alƙur'ani da Hadisan Manzon Allah SAW sun yi tsokaci da mu'ujizozi (miracles) tara da aka bai wa Annabi Musa: 1) Sandarsa 2) Hannunsa 3) Shekarun yunwa 4) Teku 5) Mamakon Ruwa 6) Fara 7) Ƙwarƙwata 8) Kwaɗi 9) Jini.

Duk waɗannan mu'ujizozi ne da Fir'auna ya kamata ya Sallamawa Annabi Musa ya yi imani da shi, amma ya ƙiya. Sai matsafan da ya gayyato domin ƙure Annabi Musa ne suka miƙa wuya, suka yi imani da Annabi Musa.

RIKICI CIKIN ADDININ ANNABI MUSA

To amma Alƙur'ani ya faɗa mana cewar Yahudu sun ce Uzair ɗan Allah ne, haka suma Nasara (Kirista) sun ce Isah ɗan Allah ne. Bayan duk abinda ke cikin sama da ƙasa halitta ce wadda Allah SWT Ya ƙaga, Ya siffanta, Ya rayar kuma ya gudanar. Kowa da komai mai ƙarewa ne banda Allah Zal Jalali wal Ikraam.

وَقَالَتِ ٱلۡيَهُودُ عُزَيۡرٌ ٱبۡنُ ٱللَّهِ وَقَالَتِ ٱلنَّصَٰرَى ٱلۡمَسِيحُ ٱبۡنُ ٱللَّهِۖ ذَٰلِكَ قَوۡلُهُم بِأَفۡوَٰهِهِمۡۖ يُضَٰهِـُٔونَ
قَوۡلَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِن قَبۡلُۚ قَٰتَلَهُمُ ٱللَّهُۖ أَنَّىٰ يُؤۡفَكُونَ

ٱتَّخَذُوٓاْ أَحۡبَارَهُمۡ وَرُهۡبَٰنَهُمۡ أَرۡبَابٗا مِّن دُونِ ٱللَّهِ وَٱلۡمَسِيحَ ٱبۡنَ مَرۡيَمَ وَمَآ أُمِرُوٓاْ إِلَّا لِيَعۡبُدُوٓاْ إِلَٰهٗا
وَٰحِدٗاۖ لَّآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۚ سُبۡحَٰنَهُۥ عَمَّا يُشۡرِكُونَ

FASSARA

Kuma Yahũdãwa suka ce: "Uzairu ɗan Allah ne."Kuma Nasãra suka ce: "Masĩhu ɗan Allah ne." Wancan zancensu ne da bãkunansu. Sunã kamã da maganar waɗanda suka kãfirta daga gabãni. Allah Yã la'ance su! Yãya aka karkatar da su?

Sun riƙi mãlamansu (Yahũdu) da ruhubãnãwansu (Nasãra) Ubannangiji, baicin Allah, kuma sun riƙi Masĩhu ɗan Maryama (haka). Kuma ba a umurce su ba fãce da su bautã wa Ubangiji Guda. Bãbu abin bautãwa fãce Shi. TsarkinSa ya tabbata daga barin abin da suke yin shirki da shi. [Surah At-Tawbah: 30-31]

Koda wasu cikin Yahudawa da Nasara basu da imanin cewa Uzair da Masihu (Annabi Isa) yayan Allah ne, to mafi yawansu suna da wannan imanin daga

wancan lokacin da wannan aya ta sauka. Shi yasa Allah SWT Ya bamu labarin su.

Anan gizo ya yi saƙar, amma bari mu ji wanene Uzair?

UZAIR

Alƙur'ani ya yi mana tsokaci kan Uzair

أَوۡ كَٱلَّذِى مَرَّ عَلَىٰ قَرۡيَةٍ وَهِىَ خَاوِيَةٌ عَلَىٰ عُرُوشِهَا قَالَ أَنَّىٰ يُحۡىِۦ هَٰذِهِ ٱللَّهُ بَعۡدَ مَوۡتِهَاۖ فَأَمَاتَهُ ٱللَّهُ مِاْئَةَ عَامٍ ثُمَّ بَعَثَهُۥۖ قَالَ كَمۡ لَبِثۡتَۖ قَالَ لَبِثۡتُ يَوۡمًا أَوۡ بَعۡضَ يَوۡمٍۖ قَالَ بَل لَّبِثۡتَ مِاْئَةَ عَامٍ فَٱنظُرۡ إِلَىٰ طَعَامِكَ وَشَرَابِكَ لَمۡ يَتَسَنَّهۡۖ وَٱنظُرۡ إِلَىٰ حِمَارِكَ وَلِنَجۡعَلَكَ ءَايَةً لِّلنَّاسِۖ وَٱنظُرۡ إِلَى ٱلۡعِظَامِ كَيۡفَ نُنشِزُهَا ثُمَّ نَكۡسُوهَا لَحۡمًاۚ فَلَمَّا تَبَيَّنَ لَهُۥ قَالَ أَعۡلَمُ أَنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَىۡءٍ قَدِيرٌ

Kõ kuwa wanda ya shũɗe a kan wata alƙarya, alhãli kuwa tana wõfintacciya a kan gadãjen rẽsunanta. Ya ce: "Yaya Allah zai rãyar da wannan a bãyan mutuwarta." Sai Allah Ya matar da shi, shẽkara ɗari; sa'an nan kuma ya tãyar da shi. Ya ce: "Nawa ka zauna?" Ya ce: "Na zauna yini ɗaya ko kuwa rabin yini." Ya ce: "A'a kã zauna shẽkara ɗari." To, ka dũba zuwa ga abincinka, da abin shanka, (kõwanensu) bai sãke ba, kuma ka dũba zuwa ga jãkinka, kuma dõmin Mu sanya ka wata ãyã ga mutãne. Kuma ka duba zuwa ga ƙasũsuwa yadda Muke mõtsarda su sa'an nan kuma Mu tufãtar da su, da nãma", To, a lõkacin da (abin) ya bayyana a gare shi, ya ce: "Ina sanin cẽwa lalle Allah a kan dukan kõme Mai ĩkõn yi ne." [Surah Al-Baqara ayah ta: 259]

Wasu daga cikin Malaman Tafsirin Alƙu'ani sun tafi akan cewar wannan mutumin da wannan Ayar take magana akai shine Uzair. Tarihi ya nuna cewar Uzair bawan Allah ne na gari mai cikakkiyar biyayya ga Addinin Annabi Musa da duk dokokin Allah waɗanda Annabi Musa ya zo da su. Ance ya rayu wajen ƙarni na biyar kafin zuwan Annabi Isa AS. Bayan an ci garin Jerusalem da yaƙi,

an dagargaza gidaje da guraren ibada na mabiya Annabi Musa, sai Uzair ya zo wucewa akan jakinsa ta gefen garin. Ganin yadda

garin Jerusalem ya koma kango shine ya ce "ta yaya Allah zai sake rayar ko tayar da wannan gari bayan mutuwarsa?" Har zuwa ƙarshen ayar.

Bayan Allah SWT Ya sake rayar da Uzairu da jakinsa, sai Uzair ya hau jakin ya shiga sabon garin da aka mayar da gininnikansa sabbi a lokacin da shi yake da jakinsa a mace. Amma babu wanda ya sani kuma babu wanda ya san shi, domin duk waɗanda suka yi zamani da shi sun mutu, sai wata tsohuwa tukub wadda ta makance domin tsufa. Ita ce kawai ta shaida shi da wata alama a kafaɗarsa shima ya shaidata. Amma duk jikokinsa sun tsufa ƙwarai saɓanin shi Allah Ya tashe shi kan ganiyarsa kamar lokacin da Allah Ya karɓi rayuwarsa, watau yafi jikokinsa ƙuruciya da kyawun jiki na matashi. Wannan ita ce Ayar da Allah Ya nuna masa da ragowar jama'ar Jerusalem - ga shi matashi amma jikokinsa tsofaffi tukub.

Kasancewar sa babban malami kuma ya tarar duk koyarwa Annabi Musa ta sakwarkwace cikin jama'ar garin, sannan Littafin Attaura shima an lalata shi lokacin rushe Jerusalem, shine ya yi ƙoƙarin sake rubuta wani littafin na Attaura daga abinda ya haddace gabani da kuma abinda yayi saura na Attaurar da ta rage.

Ganin ya daɗa farfaɗo da koyarwar Addinin Yahudanci shine jama'ar sa suka ringa girmama shi tare da kambama shi har zuwa bayan rasuwarsa karo na biyu. Bayan nan, wasu su ka ɗauke shi ɗan Allah. Amma wannan ba duk Yahudawa ne suka yarda cewa shi ɗan Allah ne ba.

Daga nan sai Tauhidi yayi rauni cikin zukatan waɗanda suke cewa Uzair ɗan Allah ne. Ganin wannan matsala Allah SWT Ya aiko da Annabi Isa domin gyara abinda ya gurɓace cikin Addinin Annabi Musa AS.

BUSHARAR ZUWAN SABON ANNABI DAGA BAKIN ANNABI MUSA, IDAN YA KAU.

Labarin zuwan sabon Annabi daga bakin Annabi Musa idan ya rasu shine kamar haka;

Deuteronomy Chapter 18: verses 15-19

15 Ubangiji, Ubangijinku zai tayar da wani Annabi daga cikinku, daga cikin ɗan uwanku (Banu Israel), kamar yadda kuka saurareni (ku ka bi ni) to shima ku saurareshi (ku bi shi).

16 Abinda ku ka bukata (roƙa) daga Ubangiji, Ubangijinku a garin Horeb rãnar (babban) Taro, cewar, kada in sake jin Muryar Ubangiji Allah na, kuma kada In sake ganin wannan Wutar don kada In mutu.

17 Sai Ubangiji ya ce mini, sun yi maganar ƙwarai abinda suka faɗa.

18 Zan tayar da wani Annabi daga cikin ɗan uwansu, kamar ka, kuma zan sanya kalmomina a cikin bakinsa, kuma ya gaya musu duk abinda Na umarce shi.

19 Kuma abinda zai auku shine, duk wanda bai saurari kalmomiNa ba, waɗanda zai faɗa da Suna Na ba, Zan tambaye shi game da su. (Da su kalmomin Zan hukunta shi ranar ƙiyama).

Waɗannan bayanan daga Attaura gaskiya ne, magana ce ƙarara babu kwane-kwane, ko kwatance-kwatance ko kame-kame (interpolation) cewar tabbas Allah zai sake aiko da sabon Annabi bayan Annabi Musa da Harun. Sai dai Allah a nan bai faɗi sunan Annabin ba ƙarara. Amma sai dai tsokaci cewar zai zo ne daga cikinsu amma na daga ɣan uwansu. Wannan zai iya kasancewa Annabi Isa ko Annabi Muhammadu SAW ake nufi.

Ko ma wanene Yake nufi daga cikin waɗannan Annabawa biyu na ƙarshe, abin mamakin shine, har yau ɗin nan da yawa daga cikin Yahudawa ko dukkansu ba su yi imani da Annabi Isa ba, bare Annabi Muhammad SAW, sai ɣan kaɗan waɗanda suka fahimci saƙon kuma suka yi aiki da shi.

Ina daɗa tuna mana cewar Annabi Musa da mahaifiyar Annabi Isa AS sun fito ne daga tsatson Annabi Ya'aƙub ɗan Annabi Ishaq, ɗan Annabi Ibrahim, haka shima Annabi Muhammad SAW ya fito ne daga tsatson Annabi Isma'il shima ɗan Annabi Ibrahim AS. Kenan ɣayan Annabi Isma'il ɣan uwan ɣayan Annabi Ishaq ne.

Saboda haka wannan wahayin ya dace da Annabi Isa AS amma kuma dai, yafi dacewa da Annabi Muhammad SAW. Saboda duk Surar da za a karanta cikin Alƙur'ani sai an fara ta "Da Sunan Allah", (kalmomin da zai faɗa da Suna Na (Ni Allah)),)banda Tauba).

بسم الله الرحمان الرحيم

Fassara: Da sunan Allah Mafi Rahama (tausayi) Mafi jin Ƙai.

Hasalima Yahudawa ne suka kama Annabi Isa suka gicciyeshi a jikin "Cross" cewar maƙaryaci ne kuma ba Manzo ba ne. Saƃanin Musulmai, mu da muka yi Imani da dukkansu ukun, Annabi Musa AS da Annabi Isa AS da Annabi Muhammad SAW.

Kamar yadda Yahudawa ba su yi imani da Annabi Isa ba (duk da Annabinsu ya umarcesu da hakan), haka suma Kiristoci ba su yi Imani da Annabi Muhammad SAW ba (duk da suma Annabinsu Isa AS ya umarce da hakan.

وَإِذۡ قَالَ عِيسَى ٱبۡنُ مَرۡيَمَ يَٰبَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ إِنِّي رَسُولُ ٱللَّهِ إِلَيۡكُم مُّصَدِّقٗا لِّمَا بَيۡنَ يَدَيَّ مِنَ ٱلتَّوۡرَىٰةِ
وَمُبَشِّرَۢا بِرَسُولٖ يَأۡتِي مِنۢ بَعۡدِي ٱسۡمُهُۥٓ أَحۡمَدُۖ فَلَمَّا جَآءَهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِ قَالُواْ هَٰذَا سِحۡرٞ مُّبِينٞ

Kuma a lõkacin da Ĩsã ɗan Maryama ya ce: "Yã Banĩlsrã'ĩla! Lalle nĩ Manzon Allah ne zuwa gare ku, mai gaskata abin da ke gaba gare ni na Attaura, kuma mai bãyar da bushãra da wani Manzo da ke zuwa a bãyãna, Sũnansa Ahmad (Mashãyabo)." To, a lõkacin da ya jẽ musu da hujjõji (shi sabon Annabin, watau Annabi Muhammad SAW), suka ce: "Wannan sihiri ne, bayyananne." [Surah Aṣ-Ṣaff: 6]

Wannan shine a dunƙule bayani kan Addinin Yahudanci na Annabi Musa AS da jama'ar sa Yahudawa.

A ƙarshe abinda yafi kamata ga Yahudawa lokacin da Annabi Isa ɗan Maryam ya baiyana, su yi Imani da shi su koma su zama mabiya Addinsa. Shike nan sun kuƀuta sun yi biyayya ga Annabi Musa AS. Amma saboda tsabar taurin kansu, suka ƙi, hasalima suka yi ƙoƙarin kashe shi a jikin "Cross". Amma saboda rashin karanta tarihi da rashin fahimtar Addininsu, wai Kiristoci Yahudu suke ɗauka aminai masoya. Allah Ya sauwaƙe kidahumanci.

وَقَوۡلِهِمۡ إِنَّا قَتَلۡنَا ٱلۡمَسِيحَ عِيسَى ٱبۡنَ مَرۡيَمَ رَسُولَ ٱللَّهِ وَمَا قَتَلُوهُ وَمَا صَلَبُوهُ وَلَٰكِن شُبِّهَ لَهُمۡۚ وَإِنَّ
ٱلَّذِينَ ٱخۡتَلَفُواْ فِيهِ لَفِي شَكّٖ مِّنۡهُۚ مَا لَهُم بِهِۦ مِنۡ عِلۡمٍ إِلَّا ٱتِّبَاعَ ٱلظَّنِّۚ وَمَا قَتَلُوهُ يَقِينَۢا

Da faɗarsu: "Lalle ne mu, mun kashe Masĩhu ĩsã ɗan Maryama Manzon Allah," alhãli kuwa ba su kashe shi ba, kuma ba su tsire shi ba, kuma amma an kamanta shi ne a garẽ su (mutuwarsa a jikin kros). Lalle ne waɗanda suka sãƀãwa jũna a cikin sha'aninsa (Annabi Isa ɗan Maryam) lalle ne, sunã shakka

daga gare, shi, bã su da wani ilimi fãce bin zato kuma ba su kashe shi ba bisa ga yaƙĩni. [Surah An-Nisāʾ: 157]

Manzon Allah SAW ya ce Yahudu sun kasu har saba'in da uku amma kaso ɗaya ne cikinsu yan Aljanna, ragowar yan Wuta ne. Duk mai Tauhidi zai iya hararo wannan kason na yan Aljanna cikin Yahudawa cewa sune waɗanda suka bi Annabi Musa lokacin da ya ke raye, har suka mutu ba su yi shirka ba, da kuma Yahudawan da su ka koma suka bi Annabi Isa ɗan Maryam lokacin da ya ke a raye, suma suka mutu ba su yi shirka ba, kuma ba su ce shi Annabi Isan ɗan Allah ne ba. Da kuma Yahudawan da suka rayu suka yi amanna da Annabi Muhammadu SAW har suka mutu kan haka, kuma ba suyi shirka ba lokacin da Annabin yake da rai, da bayan rasuwarsa har zuwa Ranar Busar Ƙaho.

A yau a duniya, Yahudu na asali tsiraru ne sai dai sun haɗa kai da maguzawan Turawa marassa Addini suna sheƙe ayarsu tare da cin karensu ko babbaka babu. Amma Allah Ya na nan a madakata.

11 - ANNABI ISA (JESUS) AS.

Annabi Isa AS an aiko shi ne ga Nasara (mutanen Nazareth). Waɗannan asallinsu dangin Yahudawa ne, Banu Isra'ila.

A yau shiga Kiristanci in ji Kiristoci shine ƙudure aƙidar cewa:

1) Allah Uba, Annabi Isa ɗa (kuma shima Allah ne), kuma dai shine Ruhi mai tsarki (wanda ya taso daga ƙabari bayan ya mutu). Wannan shi ake cewa "Trinity") - Allah ɗayan uku.

2) Mutuwar Annabi Isa da Tashin sa daga mutuwa da kuma tashin sa zuwa sama.

3) Tsarkin Coci da musharakar Waliyai (Saints) cikin al'amarinsu

4) Dawowar Annabi Isa karo na biyu da Cetonsa da kuma tabbatar da ikon sa a ban ƙasa.

5) So ko ƙaunar Annabi Isa AS, da yadda da cewar ya bayar da jinsinsa ne (Gicciye shi jikin 'cross') domin wanke Zunuban duk wani Kirista mai son na shi. Da wannan ne kawai Kirista zai shiga cikin ceton Annabi Isa AS ranar Lahira, (Salvation).

Mai karatu ya iya tambaya ina hujjojinsu cikin duk waɗannan batutuwa?

Duk da Kiristoci sun kasu ƙungiya ƙungiya tun tun tuni, amma yawancinsu duk sun yarda da waɗannan aƙidun koda basu daidaita ba kan fassarar wasu abubuwan cikin fahimtarsu ga waɗannan ƙa'idojin.

Su a gurinsu duk wanda bai yarda da waɗancan aƙidun ba, to ya kafircewa Kiristanci. Watau a yau, Musulmai duk kafirai ne a gurin Kiristoci. Saboda

farkon aƙidar Musulunci shine Tauhidi - Ɗayantakar Allah SWT Wanda bai haifa ba, kuma babu wanda ya haife Shi AWJ.

Annabi Isah AS, ya zo bayan kimanin shekaru .... da tafiyar Annabi Musa AS.

Annabi Isa AS, samuwarsa kamar samuwar Annabi Adam ne. ALLAH AWJ Ya halicci Annabi Adam ba tare da uwa ko uba ba lokacin da Allah Ya so. Ya halicci Hauwa'u da uba amma babu uwa lokacin da Ya so. Kamar haka ne Ya halicci Annabi Isa da uwa babu uba a lokacin da Ya so. In dai ka fahimci wannan, kuma ka ƙaddarawa Allah ƙarfin ikonSa na halittawa da gudanar da halittunSa duk cikin lokacin da Ya so, to babu ta yadda zaka yarda da cewar Annabi Isa ko Uzair ɗan Allah ne mai jinsi irin na Allah SWT. Duk abinda kake iya gani da idanunka a doron ƙasar nan, da cikin Teku, da sararin Subhana, halitta ce wadda Allah Ya yi da Kansa ta hanyar faɗar kawai "KUN FA YAKUUN", - "KASANCE SAI (ABIN) YA KASANCE". - "BE AND IT IS", a duk cikin lokacin da Ya so, a kuma duk bigiren da Ya so, ga kuma duk wanda Ya so, Zal Jalali wal Ikram.

Ga abinda Alƙur'ani ya faɗa game da samuwar Annabi Isa AS

إِنَّ مَثَلَ عِيسَىٰ عِندَ ٱللَّهِ كَمَثَلِ ءَادَمَ ۖ خَلَقَهُۥ مِن تُرَابٍ ثُمَّ قَالَ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ

Lalle ne misãlin Ĩsã a wurin Allah kamar misãlin Ãdama ne, (Allah) Yã halitta shi (Adam) daga turƀãya, sa'an nan kuma Ya ce masa: "Ka kasance: "Sai yana kasancewa. [Surah Āli-ʿImrān: 59]

إِذْ قَالَتِ ٱلْمَلَٰٓئِكَةُ يَٰمَرْيَمُ إِنَّ ٱللَّهَ يُبَشِّرُكِ بِكَلِمَةٍ مِّنْهُ ٱسْمُهُ ٱلْمَسِيحُ عِيسَى ٱبْنُ مَرْيَمَ وَجِيهًا فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْـَٔاخِرَةِ وَمِنَ ٱلْمُقَرَّبِينَ

A lõkacin da malã'iku suka ce "Yã Maryamu! Lalle ne Allah Yana bã ki bushãra da wata kalma daga gare Shi; sũnansa Masĩhu ĩsa ɗan Maryama, yana mai daraja a dũniya da Lãhira kuma daga Makusanta. [Surah Āli-ʿImrān: 45]

وَيُكَلِّمُ ٱلنَّاسَ فِى ٱلۡمَهۡدِ وَكَهۡلًا وَمِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ

قَالَتۡ رَبِّ أَنَّىٰ يَكُونُ لِى وَلَدٞ وَلَمۡ يَمۡسَسۡنِى بَشَرٞۖ قَالَ كَذَٰلِكِ ٱللَّهُ يَخۡلُقُ مَا يَشَآءُۚ إِذَا قَضَىٰٓ أَمۡرٗا فَإِنَّمَا يَقُولُ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ

Kuma yana yi wa mutãne magana a cikin shimfiɗar jariri, da kuma lõkacin da yana dattijo, kuma yana daga sãlihai.".

Ta ce: "Yã Ubangijina! Yãya yãro zai kasance a gare ni, alhãli kuwa wani mutum bai shãfe ni ba?" (Allah) Ya ce: "Kamar wannan ne, Allah yana halittar abin da Yake so. Idan Ya hukunta wani al'amari, sai ya ce masa, "Ka kasance!, Sai yana kasancẽwa." [Surah Āli-ʿImrān: 46-47]

وَمَرۡيَمَ ٱبۡنَتَ عِمۡرَٰنَ ٱلَّتِيٓ أَحۡصَنَتۡ فَرۡجَهَا فَنَفَخۡنَا فِيهِ مِن رُّوحِنَا وَصَدَّقَتۡ بِكَلِمَٰتِ رَبِّهَا وَكُتُبِهِۦ وَكَانَتۡ مِنَ ٱلۡقَٰنِتِينَ

Da Maryama ɗiyar Imrãna wadda ta tsare farjinta, sai Muka hũra a cikinsa (aljihun tufafin ta) daga rũhinMu (wani rai cikin rayukan dake gareMu). Kuma ta gaskata game da ãyõyin Ubangijinta da Littattafan Sa alhãli kuwa ta kasance daga mãsu tawãli'u. [Surah At-Taḥrīm: 12]

وَٱذۡكُرۡ فِى ٱلۡكِتَٰبِ مَرۡيَمَ إِذِ ٱنتَبَذَتۡ مِنۡ أَهۡلِهَا مَكَانٗا شَرۡقِيّٗا

فَٱتَّخَذَتۡ مِن دُونِهِمۡ حِجَابٗا فَأَرۡسَلۡنَآ إِلَيۡهَا رُوحَنَا فَتَمَثَّلَ لَهَا بَشَرٗا سَوِيّٗا

قَالَتۡ إِنِّيٓ أَعُوذُ بِٱلرَّحۡمَٰنِ مِنكَ إِن كُنتَ تَقِيّٗا

قَالَ إِنَّمَآ أَنَا۠ رَسُولُ رَبِّكِ لِأَهَبَ لَكِ غُلَٰمٗا زَكِيّٗا

قَالَتۡ أَنَّىٰ يَكُونُ لِى غُلَٰمٞ وَلَمۡ يَمۡسَسۡنِى بَشَرٞ وَلَمۡ أَكُ بَغِيّٗا

قَالَ كَذَٰلِكِ قَالَ رَبُّكِ هُوَ عَلَيَّ هَيِّنٞۖ وَلِنَجۡعَلَهُۥٓ ءَايَةٗ لِّلنَّاسِ وَرَحۡمَةٗ مِّنَّاۚ وَكَانَ أَمۡرٗا مَّقۡضِيّٗا

فَحَمَلَتۡهُ فَٱنتَبَذَتۡ بِهِۦ مَكَانٗا قَصِيّٗا

فَأَجَآءَهَا ٱلۡمَخَاضُ إِلَىٰ جِذۡعِ ٱلنَّخۡلَةِ قَالَتۡ يَٰلَيۡتَنِى مِتُّ قَبۡلَ هَٰذَا وَكُنتُ نَسۡيًا مَّنسِيًّا

فَنَادَىٰهَا مِن تَحۡتِهَآ أَلَّا تَحۡزَنِى قَدۡ جَعَلَ رَبُّكِ تَحۡتَكِ سَرِيًّا

وَهُزِّىٓ إِلَيۡكِ بِجِذۡعِ ٱلنَّخۡلَةِ تُسَٰقِطۡ عَلَيۡكِ رُطَبًا جَنِيًّا

فَكُلِى وَٱشۡرَبِى وَقَرِّى عَيۡنًا ۖ فَإِمَّا تَرَيِنَّ مِنَ ٱلۡبَشَرِ أَحَدًا فَقُولِىٓ إِنِّى نَذَرۡتُ لِلرَّحۡمَٰنِ صَوۡمًا فَلَنۡ أُكَلِّمَ ٱلۡيَوۡمَ إِنسِيًّا

فَأَتَتۡ بِهِۦ قَوۡمَهَا تَحۡمِلُهُۥ ۖ قَالُواْ يَٰمَرۡيَمُ لَقَدۡ جِئۡتِ شَيۡـًٔا فَرِيًّا

يَٰٓأُخۡتَ هَٰرُونَ مَا كَانَ أَبُوكِ ٱمۡرَأَ سَوۡءٍ وَمَا كَانَتۡ أُمُّكِ بَغِيًّا

فَأَشَارَتۡ إِلَيۡهِ ۖ قَالُواْ كَيۡفَ نُكَلِّمُ مَن كَانَ فِى ٱلۡمَهۡدِ صَبِيًّا

قَالَ إِنِّى عَبۡدُ ٱللَّهِ ءَاتَىٰنِىَ ٱلۡكِتَٰبَ وَجَعَلَنِى نَبِيًّا

وَجَعَلَنِى مُبَارَكًا أَيۡنَ مَا كُنتُ وَأَوۡصَٰنِى بِٱلصَّلَوٰةِ وَٱلزَّكَوٰةِ مَا دُمۡتُ حَيًّا

وَبَرًّۢا بِوَٰلِدَتِى وَلَمۡ يَجۡعَلۡنِى جَبَّارًا شَقِيًّا

وَٱلسَّلَٰمُ عَلَىَّ يَوۡمَ وُلِدتُّ وَيَوۡمَ أَمُوتُ وَيَوۡمَ أُبۡعَثُ حَيًّا

ذَٰلِكَ عِيسَى ٱبۡنُ مَرۡيَمَ ۖ قَوۡلَ ٱلۡحَقِّ ٱلَّذِى فِيهِ يَمۡتَرُونَ

مَا كَانَ لِلَّهِ أَن يَتَّخِذَ مِن وَلَدٍ ۖ سُبۡحَٰنَهُۥٓ ۚ إِذَا قَضَىٰٓ أَمۡرًا فَإِنَّمَا يَقُولُ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ

وَإِنَّ ٱللَّهَ رَبِّى وَرَبُّكُمۡ فَٱعۡبُدُوهُ ۚ هَٰذَا صِرَٰطٌ مُّسۡتَقِيمٌ

فَٱخۡتَلَفَ ٱلۡأَحۡزَابُ مِنۢ بَيۡنِهِمۡ ۖ فَوَيۡلٌ لِّلَّذِينَ كَفَرُواْ مِن مَّشۡهَدِ يَوۡمٍ عَظِيمٍ

Kuma ka ambaci Maryamu a cikin Littãfi, a lõkacin da ta tsallake daga mutãnenta a wani wuri, a gẽfen gabas.

Sa'an nan ta riƙi wani shãmaki daga barinsu. Sai Muka aika rũhinMu zuwa gare ta. Sai ya bayyana a gare ta da siffar mutum madaidaci.

Ta ce: "Lalle nĩ inã nẽman tsari ga Mai, rahama daga gare ka, idan ka kasance mai tsaron addini!"

Ya ce: "Abin sani kawai, ni Manzon Ubangijinki ne dõmin in bãyar da wani yãro tsarkakke gare ki."

Ta ce: "A inã yãro zai kasance a gare ni alhãli kuwa wani mutum bai shãfe ni ba, kuma ban kasance kãruwa ba?"

Ya ce: "Kamar wancan Ubangijinki Ya ce. Shĩ, a gare Ni mai sauƙi ne. Kuma dõmin Mu sanya shi wata alãma ga mutãne, kuma wata rahama ce daga gare Mu.' Kuma abin yã kasance wani al'amari hukuntacce."

Sai ta yi cikinsa, sai ta tsallake da shi ga wani wuri mai nĩsa.

Sai nãƙuda ta kai ta zuwa ga wani kututturen dabĩniya, ta ce "Kaitona, dã dai na mutu a gabãnin wannan kuma na kasance wani abu wulakantacce wanda aka manta!"

Sai (yãron da ta haifa) ya kira ta daga ƙarƙashinta, "Kada ki yi baƙin ciki! Haƙĩƙa Ubangijinki Ya sanya wani marmaro a ƙarƙashinki.

"Kuma ki girgiza zuwa gare ki game da kututturen dabĩnon ya zuba a kanki yanã 'ya'yan dabĩno, ruɗabi nunannu."

"Sai ki ci kuma ki sha kuma ki ji sanyi ga idãnunki. To, idan kin ga wani ɗaya daga mutãne, sai ki ce, 'Lalle nĩ, na yi alwãshin azumi dõmin Mai rahama sabõda haka bã zan yi wa wani mutum magana ba."

Sai ta je wa mutãnenta tanã ɗauke da shi. Suka ce: "Yã Maryamu! Lalle ne, haƙĩƙa kin zo da wani abu mai girma!

"Yã 'yar'uwar Hãrũna! Ubanki bai kasance mutumin alfãsha ba, kuma uwarki ba ta kasance kãruwa ba."

Sai ta yi ishãra zuwa gare shi, suka ce: "Yãya zã mu yi magana da wanda ya kasance a cikin shimfiar tsumma yanã jãrĩri?"

Ya ce: "Lalle ne, nĩ bãwan Allah ne Allah Yã bã ni Littãfi kuma Ya sanya ni Annabi."

"Kuma Yã sanya ni mai albarka a inda duk na kasance kuma Ya umurce ni da yin salla da zakka matuƙar inã da rai."

"Kuma mai biyayya ga uwãta, kuma bai sanya ni mai kaushin zũciya ba marashin alhẽri."

"Kuma aminci ya tabbata a gare ni a rãnar da aka haife ni da rãnar da nake mutũwa da rãnar da ake tãyar da ni inã mai rai."

Wancan ne Ĩsã ɗan Maryamu, maganar gaskiya wadda suke shakka a cikinta.

Bã ya kasancẽwa ga Allah Ya riƙi wani ɗã. Tsarki ya tabbata a gare shi! Idan Yã hukunta wani al'amari sai kawai Ya ce masa, "Kasance." Sai ya dinga kasan cẽwa.

"Kuma lalle Allah ne Ubangijina kuma Ubangijinku, sai ku bauta Masa. Wannan shi ne tafarki madaidaici."

Sai ƙungiyõyin suka sãƀã wa jũna a tsakãninsu. To, bõne (tsananin azaba) ya tabbata ga waɗanda suka kãfirta daga halartar yini mai girma (ƙaryata Ranar Tashin Ƙiyama). [Surah Maryam: 16-37]

Yanzu mun ji abinda Allah Ya faɗa ta harshen Annabi Musa AS cikin Attaura dangane da zuwan sabon Annabi (Deuteronomy 18:15-19), kuma mun ji abinda Allah Ya faɗa ta harshen Annabi Muhammad SAW cikin Alƙur'ani mai Tsarki akan samuwar Annabi Isa AS (Surah Maryam 19:16-37), to yanzu bari mu ji abinda Allah Ya ce ta kan harshen BawsnSa Annabi Isa AS dangane da Annabi Isan da kuma koyarwarsa cikin Sabon Alƙawari "New Testament".

ME LINJILA TA ƙUNSA A YAU.

Kamar yadda Attaura (Old Testament) ta ƙunshi ƃangarori biyar (5) haka Linjila (New Testament) ta ƙunshi ƃangarori huɗu (4) - Matthew, Mark, Luka da John - ita kaɗai. Amma idan anyi maja, an haɗa ta da Attaura, ta zama mai ƃangarori tara (9) kenan. Mai karatu ya iya tambaya cewar to ina Barnabas? Manyan Kiristocin can baya mai nisa, sun cire shi sun ƃoye domin koyarwar cikinsa babu "TRINITY" sai TAUHIDI tsantsa. Sun ce ai wannan Musulunci ne aka shigo da shi Kiristanci. Allah Sarki. Wanda Allah Ya ƃatar babu mai iya shiryar da shi.

A cikin Linjila "Old and New Testaments" na ƙirga lafazin "Ɗan mutum" - "The son of Man" har guda ɗari da goma (110), - Numbers 6, Deuteronomy 1, Joshua 3, Judges 1, Kings 1, Chronicles 1, Job 2, Psalm 4, Isaiah 2, Daniel 1, Matthew 32, Mark 15, Luke 26, John 11, Acts 1, Hebrew 1, Revelation 2, Kuma duk Annabi Isa ake nufi. Domin a nuna muku cewa shifa Annabi Isa ɗan Adam ne, ba wani ƃangare na jikin Allah ne ba.

Littafi “Book”	Dan Mutum “Son of Man”	Dan Allah “Son of God”
Attaura “Old Testament”	7	0
Linjila “New Testament”	103	46
Jumla “Total”	110	46

Ko shakka babu wannan ya nuna Annabi ISAH AS ɗan Adam ne ba ɗan Allah ba. Wannan lafazin na "ɗan Allah" cikin Sabon Alƙawari ƙari ne amma ba koyarwar Annabi ISAH ba.

Haka na ga an ambaci lafazin "Ɗan Allah" -"The son of God" sau arba'in da shida (46) a cikin dai ita Linjilar. To a nan ruɗanin da Kiristoci suka shiga shine na kasa ɗaukar ma'anar "ɗa" da nufin duk wani bawan Allah, Salihin Mutum na Gari Kamar yadda mana'anarsa ta asali take cikin Addinin Annabi Musa da suke da'awar bi sau da ƙafa. Wannan tasa aka cire lafazin "ɗa" kwata-kwata daga cikin Alƙur'ani domin kawar da wannan ruɗun da rashin fahimtar.

Kuma ban ga gurin da Annabi Isa yace; "Nine Ubangijin ku bauta mini" - "I am God Worship me" duk cikin Bible, babu. To me ya jawo wannan ruɗewar da Kiristoci suka yi har suka ɗauki Annabi Isa cewar Ubangijine? Kuma komai za su yi da sunansa, haka duk roƙo da godiya da yabo gare shi kawai suke yi.

ANNABI ISA ƊAN MARYAM, BAWAN ALLAH NE NA GARI MAI DOGARO GA ALLAH

Ku saurara ga wannan jawabi daga cikin Linjila.

Psalm 146

{146:1} Yabi Ubangijinka. Yabi Ubangiji, kai ruhina. {146:2} Lokacin da nake a raye zan yabi Ubangiji: Zan rera kirarin yabon Allahna lokacin da na kasance. {146:3} Kada ka dogara ga ɣayan sarki, haka (kada ka dogara) ga Ɗan Mutum (Isa AS) Wanda babu wani taimako daga gareshi. {146:4} Nunfashinsa yakan tafi, ya koma cikin ƙasarsa; A wannan rana duk Tunaninsa ya ƙare. {146:5} Farin ciki ga wanda ya ɗauki Allahn (Annabi) Ya'aƙub ne mai taimakonsa, wanda fatansa (da dogaronsa) yana ga Ubangijinsa Allah: {146:6} Wanda ya yi sammai, da ƙasa, da kogi, da duk abinda ke cikinsa: (Mai) Hukunci mai riƙe da

gaskiya har abada: {146:7} Wanda yake sakawa (ɗaukar fansar) waɗanda aka zalunta: Wanda yake ciyar da abinci ga mayunwaci: Ubangiji Mai yanta yan kurkuku: {146:8} Ubangiji Mai buɗe (warkar da) idon makaho: Ubangiji na ɗaga waɗanda suka rusuna: Ubangiji na son mãsu gaskiya (masu aiki na ƙwarai).

Allah a cikin wannan saƙon na nuna mana cewar shi kansa Annabi Isa yabo da tsarkake Ubangiji Allah yake yi kuma ga Allah ya dogara. Sannan ya yabi masu dogaro ga Allah Shi kaɗai Mahaliccin kowa da komai. Ba a neman taimakon kowa sai Allah Shi Kaɗai, shi yasa yace kada ka dogara ga yayan sarakuna har shi kansa Annabi Isan. Kuma ya nuna cewar Annabi Isa zai rasu har a binne shi cikin ƙasa (amma bayan ya tsufa).

RIKICI CIKIN KOYARWAR ANNABI ISA AS.

Rikici cikin Kiristanci ya somo ne cikin lokuta biyu:

1) Lokacin da Annabi Isa ya tayar da mataccen mutum ya warkar da makaho da izin Allah, wasu daga cikin jama'ar sa suka ce idan ba Allah ba ko ɗan Allah, wa ke iya tayar da matacce ya warkar da makahon da aka haifa da makanta? Saboda haka suka Kambama Annabi Isa kambamawar da ta wuce gona da iri, suka ce Annabi Isa ɗan Allah ne. Wasu suka ce a'a kawai saboda zaɓin da Allah Ya yi masa Ya ba shi damar yin hakan amma da izinin Allah.

2) Lokacin da aka gicciyeshi a jikin kros, bayan kwana uku da aka fito da shi, ragowar sahabbansa suka ganshi a wani keɓaɓɓen guri, sai wasu suka yi zaton fatalwar Annabi Isa suka gani wadda suka yi kiranta da Ruhi mai Tsarki. Shi kuwa ce musu yayi Nine dai Isa ɗan Maryam mai jini da ƙashi da tsoka bakwa gani ne? Ku kusanto ku taɓa Ni ku ji. A nanma haka wasu suka tafi akan cewar Annabi Isa mutum ne kamar kowa sai dai zaɓaɓɓe ne daga Allah da Annabta da Manzanni. Wasu kuma suka ce a'a, Annabi Isa Allah ne, ɗan Allah ne, Ruhin Allah ne - wadda shi ake kira Trinity.

Saboda haka, bayan abinda ya faru ya faru, Allah Ya sakaya (ɓoye) Annabi Isa daga idanun Yahudawa maƙiyansa, sai Barnabas ya ja zugarsa ta masu Tauhidi, Paul kuma ya ja zugarsa ta masu Shirka masu Trinity. Addinin Kiristanci ya fara rabuwa kaso biyu. Allah ne Mafi sani.

KIRISTOCIN DA SUKA ƙYAMACI DA'AWAR "ALLAH UKU" NE, "THE EBIONITES" ANTI - TRINITY CHRISTIANS.

Anan ya kamata mu yi tsokaci da wata ƙungiyar Addinin Kiristanci kafin Addinin Musulunci ya baiyana, mai suna "Ebionite" da Turanci.

Wannan sunan na "Ebionite" an ciro shi ne daga yaren Hebrew "Ebyonim" Watau Talaka ko Talakawan da su ke bin Addinin Kiristanci amma ba su yarda da "TRINITY" ba, Allah ɗayan Ukun Uku. Kamar yadda al'adar ɗan Adam ta gabata, duk lokacin da aka ce ga sabon saƙo, sabon Annabi ya zo, to masu fara yi masa mubaya'a su ne talakawan gari. Shi ya sa ragowar Yahudawa da suke kan Addinin Musa AS suke kiran jama'ar farko da tayi imani da sabon Annabi watau Annabi Isa, suke kiransu da "Ebyonim". Su waɗannan Jama'a, su ake kira kuma dai “Jew-Christians”, kuma sun ɗauki Paul a mazaunin zindiƙi wanda ya yi cushe cikin Addinin Kiristanci ya gurɓata shi. Su waɗannan jama'a sun yarda Isa bawan Allah ne na gari wanda Allah Ya zaɓa da Annabta da Manzanci. Kuma asalinsu, suna kan Addinin Annabi Musa amma da zuwan Annabi Isa, su kayi Imani da shi kuma suke riƙe da koyarwarsa ta asali.

Wannnan koyarwar ita ce wadda babban sahibin Annabi Isa mai suna Barnabas ya ringa koyarwa bayan Annabi Isa ya kau. Tarihi ya nuna cewar Linjilar Barnabas (The Gospel of Barnabas) tafi kusa da koyarwar Annabi Isa wadda ta ɗauko salo irin na Annabi Musa AS mai cike da TAUHIDI watau bautawa Allah ɗaya Tak Wanda bai haifa ba, kuma babu wanda ya haifeShi. Haka kuma tafi dacewa da koyarwar Annabi Muhammad SAW, da ke cikin Alƙur"ani.

Amma ganin cewar Lijilar Barnabas ba ta yi na'am da cushen dake cikin ragowar Littatafan Linjila dake hannu ragowar Fada da ragowar ɣan mishan ba, shine manyan Malaman Kiristoci da Shugabanni suka hana bazuwarta tare da ɗaukar duk mai ita a matsayin maƙiyin Christancin.

Ka duba ka ga yadda aka tanƙwara ƙarya, aka yi mata ado cewa dole ta zama gaskiya, sannan gaskiyar kuma aka ɓoyeta. Abinda ke faruwa cikin Musulmai kenan idan muka yi la'akari da Sufanci-ƙirƙiren ƙarya wanda babu wani dalilin Alƙur"ani ko wani Hadisi ingantaccen da ya goyi bayansu. Allah Ya sauwaƙe.

Mu sani, ƙarya komai kyanta da daɗewarta da yawan mabiyanta, tana nan akan ƙaryarta, kuma ba za ta taɓa zama gaskiya ba har abada. Wannan yana daga dalilan da Allah SWT Ya aiko da Annabi Muhammad SAW domin gyara abinda ya gurɓace cikin AddininSa, amma wasu da Shaiɗan ya yiwa khuɗubar tsiya, suke so sai sun maida hanun agogo baya.

وَقُلۡ جَآءَ ٱلۡحَقُّ وَزَهَقَ ٱلۡبَٰطِلُۚ إِنَّ ٱلۡبَٰطِلَ كَانَ زَهُوقٗا

"Kuma ka ce: "Gaskiya tã zo, kuma ƙarya ta lãlãce. Lalle ne ƙarya ta kasance lãlãtacciya." [Surah Al-Isrāʾ: 81]

Waɗannan jama'a na gari cikin Kiristoci, sun sha tsangwama da kisa daga shugabanni da manyan Malaman Kiristoci waɗanda ke da Imanin Allah ɗayan Uku ne, "Trinity" watau "Gentile Christians". Sai da aka kusa ƙarar da su "Jew Christians" daga kan doron ƙasa. "Ebionites" ko "Jew Christians" sun shiga tsaka mai wuya, gaba zaki baya siyaki. Kisa da tsangwama daga Yahudawan da basu yarda da Annabi Isa Annabin Allah ne ba, sannan kisa da tsangwama daga ragowar Kiristocin da suke da'awar Annabi Isa Allah ne, kuma Ruhi ne. Wai ta yaya mutumin da aka tsuguna aka haifeshi zai zama Allah?

Amma Bahaushe ya ce na Allah baya ƙarewa. Saboda haka dole su ƙoye Imaninsu da kuma Llittattafansu (Gospel of Barnabas) daga ragowar gama-garin mutane har takai an nemi shi (Gospel of Barnabas) an rasa tsawon waɗansu ƙarnoni, sai daga baya aka cince shi a gidan wani Tarihi a ƙasar Turai.

Irin waɗannan al'umma sun kawo har zuwa baiyanar Annabi Muhammadu SAW kuma suka yi imani da shi tare da zamowa cikakkun Musulmai cikin wannan tawaga ta Annabi Muhammad SAW. Mutane irin su ɗan uwan Nana Khadijah Matar Manzon Allah SAW mai suna Waraƙa Ibn Naufal, yana cikin irin waɗannan Kiristoci. Duba Littafina mai suna "Musulunci da Sufanci a Ifriƙiyya".

GICCIYE ANNABI ISA DA SAKA SHI CIKIN KOGON KABARI.

Matthew:

{12:40} Kamar yadda Annabi Yunus (Jonah) ya kasance a cikin kifi yini uku da dare uku, to haka Ɗan Mutum (Annabi Isa AS) zai kasance yini uku da dare uku cikin zuciyar ƙasa (kogon ƙabari).

Wannan tsokaci ne ga abinda zai faru ga Annabi ISAH AS a ƙarshen rayuwarsa ta cikin garin Nazareth, inda Yahudawa suka kafa masa ƙahon tsana.

Ayoyi sun nuna cewar Annabi Yunus (Jonah) bai mutu ba a cikin kifi, har kifin ya amayar da shi a gaɓar Teku, inda ya sake farfaɗowa daga rashin lafiyar da ya samu lokacin da yake cikin kifin. To haka Annabi Isa shima bai mutu ba lokacin da yake cikin ƙabarin tsawon kwana uku har aka fitar da shi daga ciki. Kamar Yunus kamar Ɗan Mutum (Annabi Isa AS).

Mun sani al'adar Banu Israel a wancan lokacin shine yin kogo cikin tudun ƙasa tare da ajiye gawar mamaci ciki, a matsayin shine ƙabarinsa.

Abinda ya faru shine: Lokacin da aka gicciye Annabi Isa AS jikin kros, bayan ya ɗauki lokaci a jiki sai aka sauko da shi. Akwai daga cikin sahabbansa da suka lura akwai ragowar rayuwa tattare da shi a lokacin. Saboda haka, bayan an saka shi cikin kogon (ƙabari) an rufe ƙofar da ƙaton dutse, cikin dare wasunsu sun je sun sake buɗe ƙofar ƙabarin inda suka tabbatar yana da rai, saboda haka suka ringa kai masa magani da abinci har tsawon kwana uku. Daga nan suka fitar da shi cikin dare a ɓoye daka garin zuwa inda ba a sanshi ba. A can Annabi Isan ya ci gaba da da'awarsa a ɓoye har tsufansa. Daga baya Allah Ya karɓi ransa. Inji wasu daga cikin masu Tarihi.

Amma Hadisi ya nuna cewar wani daga cikin munafukan Annabi Isa, Allah ya bashi kamannin Annabi Isa har maƙiyan Annabi Isa Yahudawa suka kama shi suka tsire. Sun ɗauka Annabi Isa ne. Wannan kuwa na da goyon bayan Ayar cikin Alƙur'ani da ta ce:

وَقَوۡلِهِمۡ إِنَّا قَتَلۡنَا ٱلۡمَسِيحَ عِيسَى ٱبۡنَ مَرۡيَمَ رَسُولَ ٱللَّهِ وَمَا قَتَلُوهُ وَمَا صَلَبُوهُ وَلَٰكِن شُبِّهَ لَهُمۡۚ وَإِنَّ ٱلَّذِينَ ٱخۡتَلَفُواْ فِيهِ لَفِي شَكّٖ مِّنۡهُۚ مَا لَهُم بِهِۦ مِنۡ عِلۡمٍ إِلَّا ٱتِّبَاعَ ٱلظَّنِّۚ وَمَا قَتَلُوهُ يَقِينَۢا

Da faɗarsu: "Lalle ne mu, mun kashe Masĩhu ĩsã ɗan Maryama Manzon Allah," alhãli kuwa ba su kashe shi ba, kuma ba su tsire shi ba, kuma amma an kamanta shi ne a garẽ su. Lalle ne waɗanda suka sãɓãwa jũna a cikin sha'aninsa lalle ne, sunã shakka daga gare shi, bã da wani ilmi ba fãce bin zato, kuma ba su kashe shi ba bisa ga yaƙĩni. [Surah An-Nisāʾ: 157]

Tafsirin: "kuma amma an kamanta shi ne a gare su." kan iya ɗaukar ma'ana guda biyu. Ta farko ita ce, an kamanta siffar Annabi Isa ga wani har suka yi tsammanin Annabi Isa ne, sai suka kama shi suka tsire. Ta biyu, an kamanta

mutuwar Annabi Isa a kan kros har kowa yayi tsammani ya mutu banda yan kaɗan daga cikin Hawariyyunsa - Sahabbansa. Allah ne Mafi sani.

Wannan aya ta nuna Allah SWT Ya ɓoye Annabi Isa daga gannansu, watau ba su iya ganin haƙiƙanin abinda ya faru da shi ba, kamar yadda Allah Ya ɓoye Annabi Muhammad SAW daga gannan Ƙuraishawa lokacin da zai fita Hijira da daddare daga Makka zuwa Madina tare da babban Sahibinsa Abubakar Assiddiƙ. Allah ne mafi sanin abinda da ya faru da Annabi Isa AS bayan Allah Ya kuɓutar da shi daga hannun azzalumai Yahudawa.

BUSHARAR ZUWAN ANNABI MUHAMMAD SAW DAGA BAKIN ANNABI ISA AS.

Daniel 7

{7:13} Na gani cikin mafarkin dare, tabbas, naga wani kamar Ɗan Mutum ya zo da tarin gajimarai na samaniya (saboda yawan jama'ar mabiya), kuma ya zo da na can baya, sai suka kusanto da shi gabansa. {7:14} Sai aka ba shi ɗaukaka da tsarki (na kyawun hali) da jama'a (masu tarin yawa), na dukkan jama'a da al'ummomi, da harsuna (yare), cewa su yi masa ɗa'a (biyayya): cewa ɗaukakarsa, ɗaukaka ce ta har abada, wanda ba za ta taɓa wucewa ba, kuma ɗaukakar da ba za a taɓa ƙarar da ita ba.

Anan Annabi Isa yayi mafarkin ganin wani Annabin kamarsa mai tarin jama'a tun daga farkon zamani har zuwa ƙarshen sa. Da kuma irin ɗaukakar da Allah SWT Ya yi masa, da kuma cewar dai shi wannan annabin an aiko shi ga dukkan Al'ummomin Duniya gaba ɗaya, ba ga ƙabilarsa kawai ba. Wannan Annabin kuwa shine Annabi Muhammadu SAW duk da cewar Annabi Isa bai ambace shi da bakinsa ba. Kuma mun sani cewar mafarkin Annabawa gaskiya ne.

Akwai Ayoyi da dama cikin Alƙur'ani mai Tsarki da suka yi tsokaci kan hakan:

هُوَ ٱلَّذِىٓ أَرۡسَلَ رَسُولَهُۥ بِٱلۡهُدَىٰ وَدِينِ ٱلۡحَقِّ لِيُظۡهِرَهُۥ عَلَى ٱلدِّينِ كُلِّهِۦ وَلَوۡ كَرِهَ ٱلۡمُشۡرِكُونَ

Shi ne (Allah) wanda Ya aiko ManzonSa (Annabi Muhammadu) da shiriya da addinin gaskiya, dõmin ya ɗaukaka shi a kan dukkan wani addini, kuma kõ dã mushirikai sun ƙi. [Surah At-Tawbah: 33]

هُوَ ٱلَّذِىٓ أَرۡسَلَ رَسُولَهُۥ بِٱلۡهُدَىٰ وَدِينِ ٱلۡحَقِّ لِيُظۡهِرَهُۥ عَلَى ٱلدِّينِ كُلِّهِۦۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ شَهِيدًا

Shĩ ne (Allah) wanda Ya aiki ManzonSa (Annabi Muhammadu) da shiriya da addinin gaskiya dõmin Ya rinjãyar da shi a kan addinai dukansu. Kuma Allah Ya isa Ya zama Mai shaida. [Surah Al-Fatḥ: 28]

وَمَآ أَرۡسَلۡنَٰكَ إِلَّا رَحۡمَةً لِّلۡعَٰلَمِينَ

Kuma ba Mu aike ka ba (Ya Muhammad) fãce dõmin wata rahama ga talikai (gaba ɗayan Al'ummar Mutum da Aljani na kowacce nahiya a duniya). [Surah Al-Anbiyāʾ: 107]

Sannan a wani wurin Annabi Isa cewa ya yi;

John:

{14:15} Idan kuna ƙaunata (ku Kiristoci), to ku tsayar da (Hukunc-Hukuncen) Dokokina. {14:16} Ni kuma zan roƙi Allah sai Ya baku wani mai kwantar muku da hankali (comforter ko praiseworthy), cewar dai, zai kasance da ku har abada.

Anan Annabi Isa yana jan kunnen mutanensa da su yi aiki da dokokinsa sosai, sau da ƙafa in har suna ƙaunarsa. Shin suna yi? Sannan ya ce zai yi addu'a domin Allah Ya aiko da wani Annabin wanda daga shi babu kuma wani Annabin. Shine fassarar - zai kasance da ku har abada, SHARI'AR sa ita ce wanzazziya har abada, domin babu sauran aiko da saƙo da kuma wani Annabin.

Allah Ya karƀi Addu'arsa ga kuma dalili cikin Alƙur'ani.

{ مَّا كَانَ مُحَمَّدٌ أَبَآ أَحَدٍ مِّن رِّجَالِكُمْ وَلَـٰكِن رَّسُولَ ٱللَّهِ وَخَاتَمَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ ۗ وَكَانَ ٱللَّهُ بِكُلِّ شَىْءٍ عَلِيمًا }

Muhammadu bai kasance uban kõwa ba daga mazanku, kuma amma shĩ yã kasance Manzon Allah kuma cikamakin Annabãwa. Kuma Allah Ya kasance Masani ga kõme. [Surah Al-Aḥzāb: 40]. Addinin Musulunci shine karƀaƀƀe a gurin Allah har zuwa ranar Busar Ƙaho.

John

{16:7} Duk da haka gaskiya nake faɗa muku; Muhimmanci gareku shine in tafi in barku: domin idan ban tafi na barku ba, Mashayabo (Ahmad)(Praiseworthy) ba zai zo muku ba; amma idan na tafi zan turo shi gareku. {16:8} Kuma idan ya zo, zai tsawatar da Duniya game da zunubi, game da gaskiya da aikin ƙwarai, da kuma hukuncin (gaskiya).

Sabon Annabin zai faiyace muku menene zunubi kuma ya tsawatar muku domin kada ku aikata, zai kuma umarce ku da gaskiya da aikin ƙwarai kuma wannan zai ɗore har abada.

Wannan ma Ayar Alƙur'ani ta bayar da gaskiyar hakan:

وَإِذْ قَالَ عِيسَى ٱبْنُ مَرْيَمَ يَـٰبَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ إِنِّى رَسُولُ ٱللَّهِ إِلَيْكُم مُّصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَىَّ مِنَ ٱلتَّوْرَىٰةِ وَمُبَشِّرًۢا بِرَسُولٍ يَأْتِى مِنۢ بَعْدِى ٱسْمُهُۥٓ أَحْمَدُ ۖ فَلَمَّا جَآءَهُم بِٱلْبَيِّنَـٰتِ قَالُوا۟ هَـٰذَا سِحْرٌ مُّبِينٌ

Kuma a lõkacin da Ĩsã ɗan Maryama ya ce: "Yã Banĩlsrã'ĩla! Lalle nĩ Manzon Allah ne zuwa gare ku, mai gaskata abin da ke gaba gare ni na Attaura, kuma mai bãyar da bushãra da wani Manzo da ke zuwa a bãyãna, Sũnansa Ahmad (Mashãyabo, Praiseworthy)." To, a lõkacin da ya jẽ musu da hujjõji, suka ce: "Wannan sihiri ne, bayyananne." [Surah Aṣ-Ṣaff: 6]

Lokacin da Annabi ya jewa da Kiristoci da Yahudawa ayoyin Allah sai da yawa suka ce wannan sihiri ne bayyananne, suka ƙi yin imani da shi sai yan kaɗan.

Duk duniya ta shaida cewa Musulmai su suke bin dokokin Allah sau da ƙafa kamar yadda suka zo cikin Alƙur'ni mai Tsarki. In Banda fisgar Shaiɗan da kuma rauni da Al'ummar Musulmi tayi, da kuma Kafiran duniya da suka sa Musulunci a gaba, ai da labarin sai yafi haka kyau. Amma Alhamdu lilLahi 'ala kulli halin.

كُنتُمْ خَيْرَ أُمَّةٍ أُخْرِجَتْ لِلنَّاسِ تَأْمُرُونَ بِٱلْمَعْرُوفِ وَتَنْهَوْنَ عَنِ ٱلْمُنكَرِ وَتُؤْمِنُونَ بِٱللَّهِ ۗ وَلَوْ ءَامَنَ أَهْلُ ٱلْكِتَـٰبِ لَكَانَ خَيْرًا لَّهُم ۚ مِّنْهُمُ ٱلْمُؤْمِنُونَ وَأَكْثَرُهُمُ ٱلْفَـٰسِقُونَ

Kun kasance mafi alhẽrin al'umma (ku Sahabbai da Musulman ƙwarai) wadda aka fitar ga mutãne kuna umurni da alhẽri (Tauhidi da aikin ƙwarai) kuma kunã hani daga abin da ake ƙi (Shirka da aikin saɓo), kuma kunã ĩmãni da Allah. Kuma dã Mutãnen Littãfi (Yahudu da Nasara) sun yi ĩmãni, lalle ne, dã (haka) yã kasance mafi alhẽri a gare su. Daga cikinsu akwai mũminai (waɗanda suka Musulunta) kuma mafi yawan su fãsiƙai ne (manyan masu keta haddin Allah). [Surah Āli-ʿImrān: 110]

12 - ANNABI MUHAMMAD SAW.

وَمَآ أَرۡسَلۡنَٰكَ إِلَّا رَحۡمَةٗ لِّلۡعَٰلَمِينَ)107 (قُلۡ إِنَّمَا يُوحَىٰٓ إِلَيَّ أَنَّمَآ إِلَٰهُكُمۡ إِلَٰهٞ وَٰحِدٞۖ فَهَلۡ أَنتُم مُّسۡلِمُونَ (108)

Kuma ba Mu aike ka ba (Ya Muhammad) fãce dõmin wata rahama ga talikai (dukkan Al'umma na Ɗan Adam da Aljan har da dabbobi).

Ka ce: "Abin sani kawai, anã yin wahayi zuwa gare ni ne, cẽwa, lalle ne, Abin bautãwarku, Abin bautãwa ne Guda (Ɗaya Tilo kuma babu kamarSa). To shin kũ mãsu mĩƙa wuya ne (ga hukunce hukuncen Allah cikin koyarwar Annabin Rahama)?" [Surah Al-Anbiyāʾ: 107-108]

Allah SWT Ya aiko Annabi Muhammad SAW da Addinin Musulunci ta hanyar Alƙur'ani da kuma bayanin Alƙur'anin, watau Sunnar Annabi SAW.

Amma wasu jama'a ta Kafirai da yan Bidi'a suna inkarin Manzancin Annabi SAW, shi ya sanya Allah AWJ Ya ce a cikin Alƙur'ani mai Tsarki;

{ وَيَقُولُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَسۡتَ مُرۡسَلٗاۚ قُلۡ كَفَىٰ بِٱللَّهِ شَهِيدَۢا بَيۡنِي وَبَيۡنَكُمۡ وَمَنۡ عِندَهُۥ عِلۡمُ ٱلۡكِتَٰبِ }

Kuma waɗanda suka kãfirta sunã cẽwa: "Ba a aiko ka ba." Ka ce, "Allah Yã isa zama shaida a tsakãnina da tsakãninku da wanda yake a wurinsa akwai ilmin Littãfi". [Surah Ar-Raʿd: 43]

Abinda ake nufi da "Littafi" cikin wannan aya, shine Attaura da Linjila waɗanda ba a jirkita ba, da kuma Alƙur'ani. Ma'anar "Wanda yake a gurinsa akwai ilimin littafi" ita ce, Yahudu ko Krista da suke karanta littattafan su cikin basira da fahimta. A ƙarshe sai su Musulunta. Haka Musulmin da yake da Ilimin Alƙur'ani, kuma yake kan Sunnar Manzo, duk sun shaida cewa lallai kai Manzo ne na Allah SWT. Amma kaga ɗan Bidi'a, yana ƙaryata Manzancin Manzon Allah ne

a fakaice, domin ya ƙirƙirowa kansa wani salon Addini na daban. Duba littafina mai suna MUSULUNCI DA SUFANCI A IFRIƘIYYA.

Shiga Musulunci tun lokacin Annabi Muhammad SAW har zuwa yanzu, shine ka sani tare da yadda da ƙudurewa a zuci tare da aiki na gaƀƀai cewa:

A) MUSULUNCI

1) Shaidawa cikin furuci da babu abin bautawa da cancanta sai Allah Shi kaɗai, kuma Annabi Muhammad SAW BawanSa ne, ManzonSa ne.

2) Tsayar da Salla guda biyar a yini da dare (cikin awa 24), a kan lokacin kowacce (kuma cikin jam'i ga namiji).

3) Azumin watan Ramadan (wata ɗaya a shekara)

4) Bayar da zakka daga mawadaci zuwa ga faƙirai da sauransu

5) Hajjin ɗakin Allah ga wanda ya sami ikon guzuri, lafiya da kyan hanya.

Duk waɗannan aiyuka ne na gaƀƀai, tun daga kan furuci da harshe na Kalmar Shahada, zuwa aikin Hajji waɗanda Annabi SAW ya koyar da su domin shine Manzon da Allah Ya aiko da saƙonsu.

Sai kuma aiki na zuci wadda ƙuduri ne, shine:

B) IMANI - shine GASKATAWAR da babu MUNAFURCI da SHAKKA ko ƙanƙani cikinta, kuma mahallin ta ZUCIYA.

1) Imani da Ƙudurewa a zuci cewa babu abin bautawa da cancanta sai Allah Shi kaɗai, kuma Annabi Muhammad SAW BawanSa ne, ManzonSa ne.

2) Imani da Annabawa da Manzannin Allah gaba ɗayansu, waɗanda na ƙarshen su, watau Cikamakinsu shine Manzon Allah Annabi Muhammad SAW.

3) Imani da Littattafan Allah waɗanda Allah Ya saukar ga ManzanninSa, na ƙarshen su shine Alƙur'ani mai Tsarki.

4) Imani da Mala'ikun Allah, cewar dai suma Bayin Allah ne waɗanda ba sa saƃo, kuma ba mataimakan Allah ne ba saboda gajiyawarSa. Allah Ya fi ƙarfin komai.

5) Imani da Ranar Sakamako, watau Tashin Ƙiyama, Ranar da Allah zai tayar da kowa, bayan mutuwar kowa domin Sakamako. In Khairan, Khairan. In Sharran, Sharran.

6) Imani da Ƙaddara mai kyau da maras kyau. Duk abinda ya sameka to tun asali haka Allah Ya ƙaddara, kuma yawanci sakamakon abinda hannayenku suka aikata ne. Mu sani cewar bai halasta mutum ya abka cikin saƃo ya ce ƙaddarar Allah ce ta gabata shi yasa ya yi haka, a'a za a kama ka da wannan laifin, saboda tun asali kana sane da haramcin sa, kawai dai Allah cikin RahamarSa Ya baka zaƃi na yin daidai ko akasin hakan. Zaƃin da ba'a baiwa Mala'iku ba.

Sai kuma Kyauta yi watau kyautata aiki na Ibada ga Allah Shi kaɗai kuma bisa koyarwar Annabi SAW:

C) KYAUTA YI.

Ka bautawa Allah kamar kana ganinSa, domin idan baka ganinSa to Shi yana ganin ka. Duk aikin da Riya ta shiga cikinsa ya ƃaci.

Sai kuma kira zuwa ga Allah AWJ shine:

D) DA'AWA

Umarni da aikata abu mai kyau (TAUHIDI da aikin Alkhairi) da kuma hani ga aikata mummuna (SHIRKA da ragowar saƀo). Watau kira zuwa ga Allah cikin Hikima da lafazi mai taushi da kuma Haƙuri cikin duk abinda ya sami bawa cikin Tafarkin Allah.

Dalilai kan duk abinda ya gabata tun daga kan A) zuwa D) na ƙunshe cikin Alƙur'ani mai Tsarki da kuma fassararsa a aikace cikin Sunnar Manzon Allah Sallallahu alaihi Wasallama wadda ke rubuce cikin ingantattun littattafan Hadisai.

Littattafan Hadisai sun ƙunshi irin su Sahihul Bukhari, Sahihu Muslim, Sunan Nasa'i, Sunan Abu Dawud, Sunan At-Tirmidhi, Sunan Ibnu Majah, Musnad Ahmad bin Hambali, Muwaƈƈa Malik da sauransu.

TARIHIN ANNABI MUHAMMAD SAW.

Tarihin Annabi Muhammad SAW ya kasu kashi uku:

1) Tarihin Rayuwarsa daga lokacin da aka haife shi zuwa shekara arba'in kafin aiko shi a matsayin Manzon Allah a cikin garin Makka, shine ake cewa lokacin Jahiliyya.

2) Tarahin Rayuwarsa daga lokacin da aka aiko shi a matsayin Manzo yana da shekara arba'in zuwa sheka goma sha uku a garin Makka. Ya rayu shekara hamsin da uku a cikin Garin Makka.

3) Tarihin Rayuwarsa bayan Hijira yana da shekara hamsin da uku, zuwa Madina, cikin shekara goma. Watau ya rayu a Garin Madina tsawon shekara goma masu albarka wadda a cikinsu ne Addinin Musulunci ya kafu.

Allahu Akbar, Manzon Allah ya rasu yana da shekara sittin da uku a duniya. Ya Allah ka ƙara daƈin salati da tsira ga AnnabinKa Annabin Rahama, Muhammad

da ahlinsa da sahabbansa masu adalci da ragowar Musulmai na gari har ya zuwa Ranar Karshe.

Duk wannan yana kunshe cikin Littattafan Sirar Annabi Muhammad SAW, "Biography of Muhammad, the Messenger of Allah".

Amma Mu zamu takaita ne daga lokacin da aka aiko shi da Manzancin da kuma kadan daga cikin irin abinda Koyarwarsa ta kunsa SAW, a cikin wannan dan littafi.

LABARIN ZUWANSA SAW CIKIN LITTATTAFAN DA SUKA GABACI ALKUR'ANI.

Tun kafin a haifi Manzon Allah SAW, Allah SWT Ya bayar da labarin zuwansa a cikin Littattafan da Allah Ya saukarwa Manzannin da suka gabace shi. Haka Sahabbansa masu daraja, suma Allah AWJ Ya bayar da labarin su da kuma siffarsu cikin Linjila da Attaura.

وَإِذْ قَالَ عِيسَى ٱبْنُ مَرْيَمَ يَـٰبَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ إِنِّى رَسُولُ ٱللَّهِ إِلَيْكُم مُّصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَىَّ مِنَ ٱلتَّوْرَىٰةِ
وَمُبَشِّرًۢا بِرَسُولٍ يَأْتِى مِنۢ بَعْدِى ٱسْمُهُۥٓ أَحْمَدُ ۖ فَلَمَّا جَآءَهُم بِٱلْبَيِّنَـٰتِ قَالُوا۟ هَـٰذَا سِحْرٌ مُّبِينٌ

"Kuma a lõkacin da Ĩsã dan Maryama ya ce: "Yã Banĩlsrã'ĩla! Lalle nĩ Manzon Allah ne zuwa gare ku, mai gaskata abin da ke gaba gare ni na Attaura, kuma mai bãyar da bushãra da wani Manzo da ke zuwa a bãyãna, Sũnansa Ahmad (Mashãyabo)." To, a lõkacin da ya jẽ musu da hujjõji, suka ce: "Wannan sihiri ne, bayyananne." [Surah Aṣ-Ṣaff: 6]

FARKO-FARKON FARA SAUKAR WAHAYI.

Waraqatu Ibn Naufal (abokin wasan Nana Khadijah ne, watau dan wan mahaifinta ne) saboda haka balarabe ne amma ya bar bautar gumaka kuma ya shiga Kiristanci na asali wanda bai yarda da "Trinity" ba, wai Allah uku ne. Ya

yi riko da koyarwar Linjilar Barnabas "Gospel of Barnabas". Saninsa da "Gospel" sosai yasa ya gano tarihin zuwan Annabi Muhammad SAW a ciki. Waraqah shine wanda Nana Khadijah ta ɗauki Manzon Allah SAW ta kai shi gabansa domin neman fatawar menene yake faruwa da shi Annabi, lokacin da aka fara yi masa Wahayi a cikin kogon Hira, kuma ya dawo gida yana mai jin tsoro da fargaba. Duk da Nana Khadijah ta kwantar masa da hankali SAW, cikin faɗinta "kai mai gaskiya ne, mai amana, mai haƙuri, mai tausayin talakawa, mai sada zumunci, saboda haka Allah ba zai bari cuta ta shafe ka ba". To amma tashi mu je gurin ɗan uwana Waraqatu domin yana da ilimin Addinin Sama (Kiristancin Allah ɗaya ne kawai ba na ukun uku ba watau Trinity)".

Ta cewa Waraqah ga ɗan ɗan uwanka nan ga abinda ya sameshi. Waraqah ya tambayi Manzon Allah SAW, cewar "me ka gani kuma me ka ji?" Bayan Manzon Allah SAW ya faɗa masa abinda ya gani, da kuma karantar da shi farkon Suratul 'Alaƙ zuwa ayoyi biyar da aka fara saukarwa daga bakin Mala'ika Jibril AS:

Suratul 'Alaƙ

بسم الله الرحمان الرحيم

ٱقۡرَأۡ بِٱسۡمِ رَبِّكَ ٱلَّذِى خَلَقَ

خَلَقَ ٱلۡإِنسَـٰنَ مِنۡ عَلَقٍ

ٱقۡرَأۡ وَرَبُّكَ ٱلۡأَكۡرَمُ

ٱلَّذِى عَلَّمَ بِٱلۡقَلَمِ

عَلَّمَ ٱلۡإِنسَـٰنَ مَا لَمۡ يَعۡلَمۡ

FASSARA

(Da sunan Allah Mafi Rahama Mafi jin ƙai)
Ka yi karatu da sunan Ubangijinka, wanda Ya yi halitta.
Ya hahitta mutum daga gudan jini.
Ka yi karatu, kuma Ubangijinka shi ne Mafi karimci.
Wanda Ya sanar (da mutum) game da alƙalami.
Ya sanar da mutum abin da bai sani ba. [Surah Al-ʿAlaq: 4-5]

Sai waraƙah ya ce wannan ne Mala'ikan da ke kawo Saƙo ga Annabawa. Saboda haka kai Annabi ne, inama lokacin da mutanenka za su fidda kai daka garin ka, ina da ragowar ƙarfi, na bada gaskiya da kai kuma na taimakeka. Sai Annabi ya ce "Au har fitar da Ni za a yi daga gari?" Waraqah yace, ai babu wanda ya zo da irin saƙon ka a baya, face sai da ya sami ƴan adawa da abokan gaba da suka kore shi daga garinsa.. Amma bayan kwana kaɗan da wannan farkon Wahayi ga Manzon Rahama, Waraqah ya ce ga garin kunan - ya rasu.

Mu sani cewar Waraqatu ba ɗan Duba ba ne, ba kuma Matsafi ko Sufiy ba ne. A'a, masanin Addinin Kiristanci ne na Haƙiƙa. Bai faɗi KALMA ƙarara ba (koda yake ya faɗeta a sakaye, sannan a daidai wannan lokacin, ba a umarci Annabi da ya tashi ya yi kira ga Addini ba), bai yi Sallah ko sau ɗaya irin ta Musulmai ba (saboda ba a farlanta Sallah a lokacin ba), amma saboda ya yi Imani da Manzon Allah SAW (kuma da ya rayu har zuwa lokacin, da ya yi -sallar da ragowar Ibadoji). Manzo SAW ya ce "Na yi mafarki da Waraqatu sanye da fararen kaya fes, saboda haka ɗan Aljanna ne. Da ba ɗan Aljanna ne ba, to da wasu nau'in kayan zan ganshi da su". Sahih Bukhari. Mun san kuma mafarkin Annabawa Gaske ne, saƃanin mafarkina da naka da nasa da na Shehunnai da Sufaye. Wannan kenan.

ANNABI MUHAMMAD SAW A MATSAYINSA NA MANZON ALLAH AWJ

Sunan Manzon Allah SAW da lafazin -Muhammad- ya zo cikin Alƙur'ani mai Tsarki sau 4. Amma Allah Ya ambace shi da sunaye cikin Alƙur'ani kamar haka; Ahmad, Rasul, Nabiy, Mudassir, Muzammil, da sauransu, sannan ana yi masa alkunya da Abul Ƙasim.

Annabi Muhammad SAW, yana cikin bayin Allah na gari matuƙa. Mutum ne, ba Aljani ba, ba kuma Mala'ika ba. Bai san gaibu ba sai abinda Allah SWT Ya sanarda shi. Haka ba shi ke arzuta kanshi da kanshi ba, face abinda Sallah SWT Ya ƙaddara masa na rayuwarsa. Sannan a matsayinsa na mutum, yana rashin lafiya, yana jin yunwa, yana cin abinci da biyan bukata na bayan gida, yana bacci, yana yin aure har da yaya mata da maza SAW. Sai dai shi, ana yi masa Wahayi, kuma bayan Allah Ya ba shi Manzanci, to Ya kuma fifita shi kan ragowar halittu da abubuwa masu yawa.

{..... ٱللَّهُ أَعۡلَمُ حَيۡثُ يَجۡعَلُ رِسَالَتَهُۥۗ.....}

"..... Allah Mafi sanin inda Yake sanya manzancinSa ne....."

[Surah Al-Anʿām: 124]

Yadda Allah SWT Ya zaɓe shi da Manzanci kuma Ya ba shi Hali mafi kyau, kamar haka ne Allah Ya zaɓa masa Sahabbai da Mata mafi zama na gari da halaiya mafi kyau akan ragowar al'umma.

Duk da haka yana nan kan matsayin sa na mutum kuma bawa amma Manzo, mai bautar Allah kamar ragowar bayin Allah da Manzannin Allah. Fifita shi da Allah Ya yi, ba shi ke nufin kuma a ɗauki Siffar Allah ko aikin Allah, a dangana masa ba. Yin hakan Shirka ne. Ka yarda ko kar ka yarda wannan kai ta shafa.

Kasancewarsa mutum shi yasa Allah SWT Ya ce shi SAW mai mutuwa ne kamar ragowar mutane.

إِنَّكَ مَيِّتٌ وَإِنَّهُم مَّيِّتُونَ

Lalle kai (Ya RasululLah) mai mutuwa ne, kuma su mã lalle mãsu mutuwa ne. [Surah Az-Zumar: 30].

Tabbas Manzon Allah SAW ya rayu a duniya kuma ya rasu ya koma ga Mahaliccinsa, kamar yadda ragowar Annabawa da Manzanni suka rasu suka koma ga Mahaliccinsu gabaninsa. Allah SWT Ya yi daɗin salati da aminci garesu baki ɗaya.

Manzon Allah SAW tsarkakakke ne daga Ubangijinsa kamar yadda yazo cikin Alƙur'ani mai Tsarki. Ba shi bukatar a ƙirƙiri ƙarya a jingina masa wai don nuna Karamarsa ko Mu'ujizarsa. Alƙur'ani da Hadisansa ingantattu sun wadatar.

Manzon Allah SAW shine mutum ɗaya tilo wadda indai kai Musulmi ne dole ka so shi fiye da kowa a doron ƙasarnan. Dole ka so shi, ka yi masa ɗa'a cikin duk abinda ya umarce ka, ko ya hanaka. Daga son Allah sai na Manzo sai na Mahaifa idan suna kan Tafarkin Manzo sai ragowar salihan bayin Allah na gari waɗanda suka yi riƙo da KITABU da SUNNAH, ba waɗanda suka ƙirƙirowa kansu ɗariƙun shirka da sharholiya ba.

Allah Ya sani cewar a cikin zamani, za a samu masu yiwa Annabi ƙarya, da masu zagin Sahabbansa da Matansa, da masu faɗa da Sunnarsa, Kai har da masu da'awar Annabta da ma Allantaka.

Shi ya sanya Allah SWT Ya ja kunnen al'umma cikin Alƙur'ani, haka Manzon Allah SAW cikin hadisansa ingantattu.

Allah Maɗaukakin Sarki Ya ce:

مَّا كَانَ مُحَمَّدٌ أَبَآ أَحَدٍ مِّن رِّجَالِكُمۡ وَلَٰكِن رَّسُولَ ٱللَّهِ وَخَاتَمَ ٱلنَّبِيِّـۧنَۗ وَكَانَ ٱللَّهُ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمًا

Muhammadu bai kasance uban kõwa ba daga mazanku, kuma amma shĩ yã kasance Manzon Allah kuma cikon Annabãwa. Kuma Allah Ya kasance Masani ga kõme. [Surah Al-Aḥzāb: 40]

وَمَا مُحَمَّدٌ إِلَّا رَسُولٞ قَدۡ خَلَتۡ مِن قَبۡلِهِ ٱلرُّسُلُۚ أَفَإِيْن مَّاتَ أَوۡ قُتِلَ ٱنقَلَبۡتُمۡ عَلَىٰٓ أَعۡقَٰبِكُمۡۚ وَمَن يَنقَلِبۡ عَلَىٰ عَقِبَيۡهِ فَلَن يَضُرَّ ٱللَّهَ شَيۡـٔٗاۗ وَسَيَجۡزِي ٱللَّهُ ٱلشَّٰكِرِينَ

Kuma Muhammadu bai zama ba face manzo lalle ne manzanni sun shũɓe a gabãninsa. Ashe idan ya mutu ko kuwa aka kashe shi, zã kujũya a kan dugaduganku? To, wanda ya jũya a kan dugadugansa, bã zai cũci Allah da kõme ba. Kuma Allah zai sãka wa mãsu gõdiya. [Surah Āli-ʿImrān: 144]

مُّحَمَّدٞ رَّسُولُ ٱللَّهِۚ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥٓ أَشِدَّآءُ عَلَى ٱلۡكُفَّارِ رُحَمَآءُ بَيۡنَهُمۡۖ تَرَىٰهُمۡ رُكَّعٗا سُجَّدٗا يَبۡتَغُونَ فَضۡلٗا مِّنَ ٱللَّهِ وَرِضۡوَٰنٗاۖ سِيمَاهُمۡ فِي وُجُوهِهِم مِّنۡ أَثَرِ ٱلسُّجُودِۚ ذَٰلِكَ مَثَلُهُمۡ فِي ٱلتَّوۡرَىٰةِۚ وَمَثَلُهُمۡ فِي ٱلۡإِنجِيلِ كَزَرۡعٍ أَخۡرَجَ شَطۡـَٔهُۥ فَـَٔازَرَهُۥ فَٱسۡتَغۡلَظَ فَٱسۡتَوَىٰ عَلَىٰ سُوقِهِۦ يُعۡجِبُ ٱلزُّرَّاعَ لِيَغِيظَ بِهِمُ ٱلۡكُفَّارَۗ وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ مِنۡهُم مَّغۡفِرَةٗ وَأَجۡرًا عَظِيمَۢا

Muhammadu Manzon Allah ne. Kuma waɓannan da ke tãre da shi (Sahabbansa) mãsu tsanani ne a kan kãfirai, mãsu rahama ne a tsakãninsu, kanã ganin su sunã mãsu rukũ'i mãsu sujada, sunã nẽman falala daga Ubangijinsu, da yardarSa. Alãmarsu tanã a cikin fuskõkinsu, daga kufan sujuda. Wannan shĩ ne siffarsu a cikin Attaura. Kuma siffarsu, a cikin Injĩla ita ce kamar tsiron shũka wanda ya fitar da rẽshensa, sa'an nan ya ƙarfafa shi, ya yi kauri, sa'an nan ya daidaita a kan ƙafãfunsa, yanã bãyar da sha'awa ga mãsu shũkar' dõmin (Allah) Ya fusãtar da kãfirai game da su. Kuma Allah Ya yi wa'adi ga waɓanda suka yi ĩmãni, kuma suka aikata ayyukan ƙwarai, daga cikinsu, da gãfara da ijãra (lada) mai girma. [Surah Al-Fatḥ: 29].

قُلۡ إِنَّمَآ أَنَا۠ بَشَرٞ مِّثۡلُكُمۡ يُوحَىٰٓ إِلَيَّ أَنَّمَآ إِلَٰهُكُمۡ إِلَٰهٞ وَٰحِدٞۖ فَمَن كَانَ يَرۡجُواْ لِقَآءَ رَبِّهِۦ فَلۡيَعۡمَلۡ عَمَلٗا صَٰلِحٗا وَلَا يُشۡرِكۡ بِعِبَادَةِ رَبِّهِۦٓ أَحَدَۢا

Ka ce: "Nĩ, mutum ne kawai kamarku, anã yin wahayi zuwa gare ni cewa: Lalle ne, Abin bautawarku, Abin bautawa Guda ne, sabõda haka wanda ya yanã fãtan hadƙuwa da Ubangijinsa, to, sai ya yi aiki na ƙwarai. Kuma kada ya hadƙa kõwa ga bauta wa Ubangijinsa." [Surah Al-Kahf: 110]

وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ إِلَّا رِجَالٗا نُّوحِيٓ إِلَيۡهِمۡۖ فَسۡـَٔلُوٓاْ أَهۡلَ ٱلذِّكۡرِ إِن كُنتُمۡ لَا تَعۡلَمُونَ

بِٱلۡبَيِّنَٰتِ وَٱلزُّبُرِۗ وَأَنزَلۡنَآ إِلَيۡكَ ٱلذِّكۡرَ لِتُبَيِّنَ لِلنَّاسِ مَا نُزِّلَ إِلَيۡهِمۡ وَلَعَلَّهُمۡ يَتَفَكَّرُونَ

Kuma ba Mu aika daga gabaninka ba (Ya Rasulullah), fãce wadƙansu mazãje Muna yin wahayi zuwa gare su. Sai ku tambayi mutãnen Ambato idan kun kasance ba ku sani ba.

Da hujjõji bayyanannu da littattafai kuma Mun saukar da Ambato (Alƙur'ani) zuwa gare ka (Ya Muhammad), dõmin ka bayyanawa mutãne abin da aka sassaukar zuwa gare su, kuma don ƙammãnin su, su yi tunãni. [Surah An-Naḥl: 43-44]

هُوَ ٱلَّذِي بَعَثَ فِي ٱلۡأُمِّيِّـۧنَ رَسُولٗا مِّنۡهُمۡ يَتۡلُواْ عَلَيۡهِمۡ ءَايَٰتِهِۦ وَيُزَكِّيهِمۡ وَيُعَلِّمُهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡحِكۡمَةَ وَإِن كَانُواْ مِن قَبۡلُ لَفِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ

Shĩ ne wanda Ya aika, a cikin mabiya al'ãdu (Larabawa), wani Manzo (Annabi Muhammad SAW) daga gare su yanã karanta ãyõyin Sa a kansu, kuma yanã tsarkake su, kuma yanã sanar da su littafin (Alƙur'ani) da hikimarsa (Sunnah) kõ da yake sun kasance daga gabãninsa lalle sunã a cikin ƙata bayyanãnna. [Surah Al-Jumuʿah: 2]

وَمَا صَاحِبُكُم بِمَجۡنُونٖ

Kuma abokinku ba mahaukaci ba ne. [Surah At-Takwīr: 22]

نٓ وَٱلۡقَلَمِ وَمَا يَسۡطُرُونَ

مَآ أَنتَ بِنِعۡمَةِ رَبِّكَ بِمَجۡنُونٖ

وَإِنَّ لَكَ لَأَجۡرًا غَيۡرَ مَمۡنُونٖ

وَإِنَّكَ لَعَلَىٰ خُلُقٍ عَظِيمٖ

Ñ. Na rantse da alƙalami da abin da (marubũta) suke rubũtãwa.

Kai, sabõda ni'imar Ubangijinka, bã mahaukaci kake ba.

Kuma, lalle, haƙĩka kanã da lãdar da bã ta yankewa.

Kuma, lalle haƙiƙa kana a kan hãlãyen kirki, manya. [Surah Al-Qalam: 1-4]

قُل لَّآ أَقُولُ لَكُمۡ عِندِي خَزَآئِنُ ٱللَّهِ وَلَآ أَعۡلَمُ ٱلۡغَيۡبَ وَلَآ أَقُولُ لَكُمۡ إِنِّي مَلَكٌۖ إِنۡ أَتَّبِعُ إِلَّا مَا يُوحَىٰٓ إِلَيَّۚ قُلۡ هَلۡ يَسۡتَوِي ٱلۡأَعۡمَىٰ وَٱلۡبَصِيرُۚ أَفَلَا تَتَفَكَّرُونَ

Ka ce: "Ba zan ce muku, a wurina akwai taskõkin Allah ba. Kuma ba ni sanin gaibi, kuma ba ni gaya muku cẽwa ni malã'ika ne. Ba ni bi, fãce abin da ake yiwo wahayi zuwa gare ni." Ka ce: "Shin, makãho da mai gani sunã daidaita? Shin fa, ba ku yin tunãni?" [Surah Al-Anʿām: 50]

قُل لَّآ أَمۡلِكُ لِنَفۡسِي ضَرّٗا وَلَا نَفۡعًا إِلَّا مَا شَآءَ ٱللَّهُۗ لِكُلِّ أُمَّةٍ أَجَلٌۚ إِذَا جَآءَ أَجَلُهُمۡ فَلَا يَسۡتَـٔۡخِرُونَ سَاعَةٗ وَلَا يَسۡتَقۡدِمُونَ

Ka ce: "Ba na mallaka wa kaina wata cũta, haka kuma wani amfãni, sai abin da Allah Ya so. Ga kõwace al'umma akwai ajali, idan ajalinsu ya zo, to, bã zã su yi jinkiri daga gare shi ba, kõ dã sã'ã guda, kuma bã zã su gabãta ba." [Surah Yūnus: 49]

مَّآ أَفَآءَ ٱللَّهُ عَلَىٰ رَسُولِهِۦ مِنۡ أَهۡلِ ٱلۡقُرَىٰ فَلِلَّهِ وَلِلرَّسُولِ وَلِذِي ٱلۡقُرۡبَىٰ وَٱلۡيَتَٰمَىٰ وَٱلۡمَسَٰكِينِ وَٱبۡنِ ٱلسَّبِيلِ كَيۡ لَا يَكُونَ دُولَةَۢ بَيۡنَ ٱلۡأَغۡنِيَآءِ مِنكُمۡۚ وَمَآ ءَاتَىٰكُمُ ٱلرَّسُولُ فَخُذُوهُ وَمَا نَهَىٰكُمۡ عَنۡهُ فَٱنتَهُواْۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۖ إِنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ

Abin da Allah Ya sanya shi ganĩma ga Manzon Sa dagamutãnen ƙauyukan nan, to, na Allah ne, kuma na Manzon Sa ne kuma na mãsu dangantaka da mãrayu da miskĩnai da ɗan hanya* (matafiyi) ne dõmin kada ya kasance abin shãwãgi a tsakãnin mawadãta daga cikinku kuma abin da Manzo ya bã ku, to, ku kama shi, kuma abin da ya hane ku, to, ku bar shi. Kuma ku bi Allah da taƙawa. Lalle, Allah, Mai tsananin uƙũba ne. [Surah Al-Ḥashr: 7]

لَّقَدۡ كَانَ لَكُمۡ فِي رَسُولِ ٱللَّهِ أُسۡوَةٌ حَسَنَةٞ لِّمَن كَانَ يَرۡجُواْ ٱللَّهَ وَٱلۡيَوۡمَ ٱلۡأٓخِرَ وَذَكَرَ ٱللَّهَ كَثِيرٗا

Lalle, abin kõyi mai kyau ya kasance gare ku daga Manzon Allah, ga wanda ya kasance yanã fãtan rahamar Allah da Rãnar Lãhira, kuma ya ambaci Allah da yawa. [Surah Al-Aḥzāb: 21]

Wannan aya raddi ce ga masu cewa a yi watsi da duk littattafan hadisai a kama irin koyarwarsu da Shaiɗanu suka ɗora su akai, irin su Mai Tatsine da yaransa.

Annabi shine wanda Allah Ya ce "ya ce":

قُلۡ أَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ ٱلرَّسُولَۖ فَإِن تَوَلَّوۡاْ فَإِنَّمَا عَلَيۡهِ مَا حُمِّلَ وَعَلَيۡكُم مَّا حُمِّلۡتُمۡۖ وَإِن تُطِيعُوهُ تَهۡتَدُواْۚ وَمَا عَلَى ٱلرَّسُولِ إِلَّا ٱلۡبَلَٰغُ ٱلۡمُبِينُ

Ka ce: "Ku yi ɗã'ã ga Allah kuma ku yi ɗã'ã ga Manzo. To, idan kun jũya, to, a kansa akwai abin da aka aza masa kawai, kuma a kanku akwai abin da aka aza muku kawai, Kuma idan kun yi masa ɗã'ã za ku shiryu. Kuma bãbu abin da yake a kan Manzo fãce iyarwa (isarwa) bayyananna." [Surah An-Nūr: 54]

Manzo SAW Ya rayu shekaru arba'in a garin Makka sannan Allah SWT Ya aiko shi a matsayin Manzo kuma ya rayu shekara goma sha ukun farko da Manzanci a dai cikin garin Makkan, yana mai kira ga Tauhidi kawai. Saboda ya tashi cikin garin Makka tare da ganin Gumaka ɗari uku da sittin cikin ɗakin Ka'aba. Bayan tsangwama takai tsangwama daga Kafiran Makka, sai Allah SWT Ya yi masa izinin yin Hijira shi da Muminai zuwa garin Madina, inda

Musulunci ya sami kafuwa da ƙarfi cikin Shekaru goman da Manzon Allah SAW Ya yi ciki. Alhamdu lilLahi.

Lallai Annabi Muhammadu SAW Manzo ne, kuma ya isar da manzacinsa har lokacin da ya yiwa Sahabbansa khudubar ban kwana lokacin Hajjin ban kwana, a ƙarshe ya ke tambayar Sahabbai; "Shin a Ranar Tashin Ƙiyama idan an tambaye ku game da Ni me za ku faɗa?" Sahabbai suka amsa masa da cewa za su ce a Ranar "Lallai kai Manzon Allah ne kuma ka isar da Saƙon da aka baka don isarwa". (Da jin amsar Sahabbai), Sai Manzon Allah ya ɗaga ɗan yatsarsa manuniya zuwa sama sannan yayi nuni ga Sahabbai ya ce "Ya Allah Ka shaida, Ya Allah Ka shaida, Ya Allah Ka shaida" har sau uku, (watau ya isar da saƙo ga waɗannan bayi naSa Sahabbai). Duba cikakken Hadithin (Hijjatul Wada'i) cikin Sahihul Muslim, Sunan Abi Dawood, da Sunan Ibn Majah.

GINSHIƘAN KOYARWAR ANNABI MUHAMMAD SAW.

Ita ce 1) TAUHIDI, 2) TSORON ALLAH, 3) FAƊIN GASKIYA, 4) RIƘON AMANA, 5) SOYAYYA TSAKANIN MUMINAI, da 6) GUJEWA SHIRKA, da SAƁO KOWANNE IRI NE. Domin a gudu tare a tsira tare.

1) TAUHIDI

Musuluncin da aka aikowa Annabi kuma ya koyar da shi.

".....A yau Nã kammalã muku addininku, Kuma Nã cika ni'imaTa a kanku, Kuma Nã yarda da Musulunci ya zama addini a gare ku....." Ma'ida aya ta 3.

Wannan aya an saukar da ita ranar Arafat shekarar Hajin ban kwana.

Musulunci shine faɗin ka "La ilaha illalLah, Muhammadur RasululLah". Wannan ita ake cewa Kalmar Shahada. Da ita ake shiga Musulunci, kuma ta ƙunshi ƃangare biyu; na farko janibin Allah AWJ, na biyu janibin Manzon Allah SAW.

Ma'ana:

1) Babu wani abinda ya cancanci a bauta masa face Allah Shi kaɗai. Shi kaɗai zai Shar'anta a yi, a yi, a bari, a bari, tare da ƙauna girmamawa, tsarkakewa, fatan samun rahama da jin ƙai da tsoron fushinSa da azabarSa JJH. Duk wannan Shari'a tana ƙunshe cikin Alƙur'ani mai Tsarki.

2) Babu da ɗai wani da zai koyar da wannan Ibada ta bauta face wanda aka aiko shi da ita, watau Manzon Allah SAW. Duk bayanan da Manzon Allah SAW ya yi domin fassara ma'anonin Alƙur'ani da aiki da shi, suna ƙunshe cikin Sunnar sa wadda aka rubuce cikin littattafan Hadisai. Dole a san shi SAW, kuma a so shi, ayi masa biyayya cikin duk umarni ko hanin da ya yi, a gaskata shi cikin duk abinda ya bada labari na gaibu da zahiri. Wallahi duk wanda ka bi cikin sha'anin Addini a yau, ba Manzon Allah SAW ba, ka kama ƙafar wala. Ka mutu ka halaka duniya da lahira. Allah Ya sauwaƙe.

3) Furta wannan Kalma da gaskiya, ya wajabta kuma yin aiki da ita cikin ɓoye da sarari. Aiyukan nan kuma sun kasu kashi biyu - Ayyukan zuci na ɓoye (Imani da: Allah, Mala'iku, Manzanni, Littattafai, Ranar Ƙarshe, Ƙaddara mai kyau da maras kyau), da Ayyukan gaɓɓai na fili (Furta Kalma, Salla, Azumi, Zakka, Hajji). Ayyuka na fili, su suke nuni ga gaskiyar gasgatawar zuciyar mutum ga Musulunci. Ɗoriya kan wannan kuma sai kyautatawa cikin ayyukan can, watau Ihsani (yi domin Allah kamar kana ganinSa ga Shi gaba gareka), kuma bisa koyarwar Manzo Allah SAW kawai.

Dalili kan wannan shine, faɗin Allah SWT;

فَٱعۡلَمۡ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱللَّهُ

Ka sani cewar babu abin bautawa da cancanta sai Allah..... Suratu Muhammad aya ta 19.

مُّحَمَّدٌ رَّسُولُ ٱللَّهِ

Muhammadu Manzon Allah ne. Fathi aya ta 29.

وَمَآ أُمِرُوٓاْ إِلَّا لِيَعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ حُنَفَآءَ وَيُقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤۡتُواْ ٱلزَّكَوٰةَۚ وَذَٰلِكَ دِينُ ٱلۡقَيِّمَةِ

Kuma ba a umarce su da kome ba fãce bauta wa Allah suna mãsu tsarkake addinin gare Shi, mãsu karkata zuwa ga addinin gaskiya, kuma su tsai da salla kuma su bãyar da zakka, kuma wannan shi ne addinin waɗanda suke a kan hanyar ƙwarai. [Surah Al-Bayyinah: 5]

هُوَ ٱلۡحَيُّ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ فَٱدۡعُوهُ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَۗ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ

Shĩ ne Mai rai (Wadda ba Ya mutuwa), bãbu abin bautãwa fãce Shi. Sabõda haka ku kira Shi, kunã mãsu tsarkake addini a gare Shi. Gõdiya ta tabbata ga Allah Ubangijin halittu. [Surah Ghāfir: 65]

Jan kunne kada a rarraba a zama ƙungiya ƙungiya.

Allah SWT cikin IliminSa Ya san za a rarrabu cikin Addini, a zama ƙungiya-ƙungiya shi yasa Ya ke ja mana kunne cikin Iittafin Sa mai Tsarki.

وَأَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَلَا تَنَٰزَعُواْ فَتَفۡشَلُواْ وَتَذۡهَبَ رِيحُكُمۡۖ وَٱصۡبِرُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلصَّٰبِرِينَ

Kuma ku yi ɗã'a ga Allah da ManzonSa, kuma kada ku yi jãyayya har ku raunana kuma iskarku ta tafi, kuma ku yi haƙuri. Lalle ne Allah Yanã tãre da mãsu haƙuri. [Surah Al-Anfāl: 46]

وَلَا تَكُونُواْ كَٱلَّذِينَ تَفَرَّقُواْ وَٱخۡتَلَفُواْ مِنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَهُمُ ٱلۡبَيِّنَٰتُۚ وَأُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ عَذَابٌ عَظِيمٌ

Kuma kada ku kasance kamar waɗanda suka rarrabu kuma suka sãƀã wa jũna, bãyan hujjõji bayyanannu sun je musu kuma waɗannan sunã da azãba mai girma. [Surah Āli-ʿImrān: 105].

وَأَنَّ هَٰذَا صِرَٰطِى مُسۡتَقِيمًا فَٱتَّبِعُوهُۖ وَلَا تَتَّبِعُواْ ٱلسُّبُلَ فَتَفَرَّقَ بِكُمۡ عَن سَبِيلِهِۦۚ ذَٰلِكُمۡ وَصَّىٰكُم بِهِۦ لَعَلَّكُمۡ تَتَّقُونَ

Kuma lalle wannan ne tafarkĩNa, yana madaidaici: Sai ku bĩ shi, kuma kada ku bi wasu hanyõyi, su rarrabu ku daga hanyãTa. Wannan ne Allah Ya yi muku wasiyya da shi tsammãninku, kunã yin taƙawa. [Surah Al-Anʿām: 153]

2) TSORON ALLAH

أَنِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَٱتَّقُوهُ وَأَطِيعُونِ

"Cewa ku bauta wa Allah, ku ji tsõron Sa, kuma ku bĩ ni." [Surah Nūḥ: 3]

فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ مَا ٱسۡتَطَعۡتُمۡ وَٱسۡمَعُواْ وَأَطِيعُواْ وَأَنفِقُواْ خَيۡرٗا لِّأَنفُسِكُمۡۗ وَمَن يُوقَ شُحَّ نَفۡسِهِۦ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ

Sai ku bi Allah da taƙawa gwargwadon abin da kuka sãmi ĩko. Kuma ku saurãra kuma ku yi ɗã'ã, kuma ku ciyar, ya fi zama alhẽri gare ku. Kuma wanda ya sãƀãwa rõwar ransa, to, waɗannan sũ ne mãsu babban rabo. [Surah At-Taghābun: 16]

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَلۡتَنظُرۡ نَفۡسٞ مَّا قَدَّمَتۡ لِغَدٖۖ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ إِنَّ ٱللَّهَ خَبِيرُۢ بِمَا تَعۡمَلُونَ

Yã kũ waɗanda suka yi ĩmãni! Ku bi Allah da taƙawa kuma rai ya dũbi abin da ya gabãtar dõmin gõbe, kuma ku bi Allah da taƙawa. lalle Allah, Mai ƙididdigewa ne ga abin da kuke aikatãwa. [Surah Al-Ḥashr: 18]

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَءَامِنُواْ بِرَسُولِهِۦ يُؤۡتِكُمۡ كِفۡلَيۡنِ مِن رَّحۡمَتِهِۦ وَيَجۡعَل لَّكُمۡ نُورٗا تَمۡشُونَ بِهِۦ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ

Yã kũ waɗanda suka yi ĩmãni! Ku bi Allah da taƙawa, ku yi ĩmãni da Manzon Sa* Ya bã ku rabo biyu daga rahamar Sa, kuma Ya sanya muku wani haske

wanda kuke yin tafiya da shi, kuma Ya gãfarta muku. Kuma Allah Mai gãfara ne, Mai rahama. [Surah Al-Ḥadīd: 28]

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنَّا خَلَقۡنَـٰكُم مِّن ذَكَرٖ وَأُنثَىٰ وَجَعَلۡنَـٰكُمۡ شُعُوبٗا وَقَبَآئِلَ لِتَعَارَفُوٓاْۚ إِنَّ أَكۡرَمَكُمۡ عِندَ ٱللَّهِ أَتۡقَىٰكُمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌ خَبِيرٞ

Yã kũ mutãne! Lalle ne Mũ, Mun halitta ku daga namiji da mace, kuma Muka sanya ku dangõgi da kabĩlõli, dõmin ku san jũna. Lalle mafĩfĩcinku daraja a wurin Allah, (shĩ ne) wanda yake mafĩfĩcinku a taƙawa. Lalle nẽ Allah Masani ne, Mai ƙididdigẽwa. [Surah Al-Ḥujurāt: 13]

3) GASKIYA

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَكُونُواْ مَعَ ٱلصَّـٰدِقِينَ

Ya ku waɗanda suka yi ĩmãni! Ku bi Allah da taƙawa, kuma ku kasance tãre da mãsu gaskiya. [Surah At-Tawbah: 119]

لِّيَجۡزِيَ ٱللَّهُ ٱلصَّـٰدِقِينَ بِصِدۡقِهِمۡ وَيُعَذِّبَ ٱلۡمُنَـٰفِقِينَ إِن شَآءَ أَوۡ يَتُوبَ عَلَيۡهِمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ غَفُورٗا رَّحِيمٗا

Dõmin Allah Ya sãka wa masu gaskiya da gaskiyarsu, kuma Ya azabtar da munafukai idan Ya so, ko Ya karɓi tũba a kansu. Lalle, Allah Ya kasance Mai gãfara, Mai jin ƙai. [Surah Al-Aḥzāb: 24]

Hadith daga Sahihul Bukhari

Faɗin Allah SWT "Ya ku waɗanda suka yi ĩmãni! Ku bi Allah da taƙawa, kuma ku kasance tãre da mãsu gaskiya". [Surah At-Tawbah: 119]

4678. An rubuto daga 'Abdullahi bin Ka'aba yace "Na ji Ka'a bin Malik yana bayar da labarin yaƙin Tabuka lokacin bai fita tare da rundunar yaƙi ba, "Na rantse da Allah ban san wani mutum da Allah Ya taimakeshi da faɗar gaskiya ba fiye da Ni. Tun lokacin da na faɗi gaskiyar (abinda ya hana Ni fita yaƙi) ga

Manzon Allah SWT har zuwa yau ban taƀa nufin faɗar ƙarya ba". Kuma Allah SWT Ya baiyana wa ManzonSa: "ƙiƙiƙa Allah Ya gafarta wa Annabi da Muhajirun.... har zuwa.... kuma ku zamo tare da masu GASKIYA (cikin maganganunku da aiyukansu)"". V.9:117-119 Duba Bukhari mujalladi na 5, Hadith na 4418.

2681. 'Abdullahi bin Abbas RAm ya rubuto cewar: "Abu Sufyan ya faɗa mini cewar Hirakil ya ce masa "lokacin dana tambayeka dame-dame shi (Muhammad) yake umartarku? Ka ce yana umartarku da ku tsayar da Sallah (biyar da ita akan lokacinta), ku faɗi gaskiya, ku kame kanku daga fasiƙanci, ku cika alƙawarori, ku bayar da amanonin da aka baku (kada ku ci)". Sai Hirakil ya ƙara da cewa, "Wanɗannan tabbas sune nagartatun ɗabi'un duk wani Annabi"".

6094. 'Abdullahi RA ya ce: Annabi ya ce, "Gaskiya takan kai mutum ga Nagarta (tsoron Allah da duk wani aikin ɗa'a), kuma Nagarta takan kai mutum Aljannah, kuma mutum ba zai gushe yana faɗar gaskiya ba har sai ya zamo Assiddiƙ. Ƙarya kuwa tana kai mai ita zuwa ga fajirci (mugunta, ƙera, hassada, da duk wani mummunan abu), kuma fajirci Wuta yake kaiwa, kuma mutum ba zai gushe yana ƙarya ba, har sai an rubuta shi gaba ga Allah a matsayin maƙaryaci".

Hadith.

An karƀo daga Rib'iyi bin Hisham cewa ya ji Sayyiduna Aliyu RA cikin wata khuɗuba da ya ke bayarwa yace: Manzon Allah SAW ya ce "Kada ku faɗi ƙarya game da Ni, domin duk wanda ya faɗi ƙarya game da Ni zai shiga Wuta. Muslim ne ya rubuto.

Ƙarin bayani.

Allahu Akbar malam kaji koyarwar Fiyayyen Halitta. Ta yadda ya ɗaure kuma ya tsare Addinin Musulunci. Wannan shi ake kira da AMANAR ILIMI, ka bayar da shi yadda yake, babu ragi, babu ƙari. SAW.

Duk wanda ya ce Annabi ya ce kaza-da-kaza, alhali Annabin bai faɗa ba, to ya shiga uku, Wutar Jahannama ɗoɗar babu kwana babu taka burki.

Haka kuma, duk wanda Annabi ya riga ya faɗi kaza-da-kaza, amma ya ƙaryata, yace a'a Annabin bai ce kaza-da-kaza ɗin ba, To shima ya yiwa Annabin Rahma ƙarya, kuma Wutar Jahannama ita ce makomarsa ɗoɗar babu kwana babu jan burki.

Musussuka da ragowar ɣan ƙala ƙato masu ƙaramin sani ƙuƙumi ne da Sufaye (masu cewa Annabi ya basu wata Ibada a mafarki ko a baiyane ƙarara ko Masu da'awar wani Fathi (Ilhama ko Wahayi)) ina aka kwana? Allah Ya sauwaƙe.

Saboda haka Addinin Musulunci tuni yake a ƙaiyade. Babu ragi babu daɗi. Duk wanda zai yi magana kan Addinin Musulunci ya ji tsoron Allah, hujjarsa ta zama daga cikin Alƙur'ani da Sunnar Manzon Allah SAW. Idan babu stampi da goyon bayan Alƙur'ani ko Sunnar Fiyayyen Halitta, to Kasan cewar wannan abin "kitabur Ra'asi" ne watau molon ka ne kawai. Ya Allah! muna neman shiriya daga gareKa zuwa ga Hanya Madaidaiciya, da kariya daga faɗawa cikin hanyar da wasu mutane ke bi ta molon ka, babu Ayar Alƙur'ani babu Hadisin Manzon Allah SAW.

4) AMANA

Amana sifa ce ta Siddiƙai da Annabawan Allah da ManzanninSa waɗanda Ya bamu labarin su cikin Alƙur'aninSa mai Tsarki.

إِذْ قَالَ لَهُمْ أَخُوهُمْ نُوحٌ أَلَا تَتَّقُونَ

إِنِّى لَكُمْ رَسُولٌ أَمِينٌ

A lõkacin da Dan uwansu Nuhu ya ce musu, "Bã zã ku ji tsoron Allah ba?"

"Lalle ne, zuwa gare ku, ni Manzo ne amintacce." (Mai Amana) [Surah Ash-Shuʿarāʾ: 106-107]

Haka Allah Ya bamu labarin Annabi Hudu, Annabi Saluh, Annabi Luƙ, Annabi Shu'aib, Annabi Musa ASm.

Annabi Muhammad SAW kuwa, tun kafin a ba shi Manzanci, jama'arsa ta Ƙuraish suke masa laƙabi da Al-amin - Amintacce, mai amana.

Allah SWT Ya ci gaba da cewa cikin Alƙur'ani:

إِنَّ ٱللَّهَ يَأۡمُرُكُمۡ أَن تُؤَدُّواْ ٱلۡأَمَٰنَٰتِ إِلَىٰٓ أَهۡلِهَا وَإِذَا حَكَمۡتُم بَيۡنَ ٱلنَّاسِ أَن تَحۡكُمُواْ بِٱلۡعَدۡلِۚ إِنَّ ٱللَّهَ نِعِمَّا يَعِظُكُم بِهِۦٓۗ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ سَمِيعَۢا بَصِيرٗا

Lalle ne Allah Yanã umartarku ku bãyar da amãnõni zuwa ga mãsu sũ. Kuma idan kun yi hukunci a tsakãnin mutãne, ku yi hukunci da ãdalci. Lalle ne Allah, mãdalla da abinda Ya ke yi muku wa'azi da shi. Lalle ne Allah Yã kasance Mai ji ne, Mai gani. [Surah An-Nisāʾ: 58].

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَخُونُواْ ٱللَّهَ وَٱلرَّسُولَ وَتَخُونُوٓاْ أَمَٰنَٰتِكُمۡ وَأَنتُمۡ تَعۡلَمُونَ

Yã kũ waƙanda suka yi ĩmãni! Kada ku yaudari Allah da ManzonSa, kuma ku yaudari amãnõninku, alhãli kuwa kunã sane. [Surah Al-Anfāl: 27]

وَٱلَّذِينَ هُمۡ لِأَمَٰنَٰتِهِمۡ وَعَهۡدِهِمۡ رَٰعُونَ

Kuma waƙanda suke, sũ ga amãnõninsu da alkawarinsu mãsu tsarẽwa ne. (Sune suka Rabauta) [Surah Al-Muʾminūn: 8]

Hadith

6095. Abu Hurairah RA yace, Manzon Allah SAW ya ce “Alamomin Munafuki uku ne: 1) Idan ya yi magana sai ya fadi karya. 2) Idan ya yi alkawari sai ya saba. 3) Idan an bashi amana sai ya ci”. Sahih Bukahari.

[363] An rubuto cewar Al-Alhasan ya ce, "Ubaidullahi bin Ziyad ya ziyarci Ma'ƙil bin Yasar Al-Muzani lokacin rashin lafiyarsa ta ƙarshe. Maƙil yace: 'Zan faɗa muku wani Hadisi wanda na ji daga Manzon Allah SAW da ina da masaniyar zan tashi daga wannan cuta da bazan faɗa muku ba. Na ji Manzon Allah SAW ya xe: "Babu wani mutum da Allah zai shugabantar kan wasu mutane ya cuce su (ya ci amanarsu) face Allah Ya haramta masa shiga Aljanna". Sahih Muslim.

893. Annabi (S.A.W.) yace; Haƙiƙa kowannenku mai kiwo ne sannan zaa tambaye shi a bisa abinda aka ba shi kiwo. Shugaba mai kiwo ne akan jamaar sa, kuma tabbas zaa tambaye shi lamarinsu. Mai gida mai kiwo ne na jamaar gidansa, kuma zaa tambaye shi game da abinda ya gudanar a cikin gidansa. Uwar gida mai kiwo ce a cikin gidan mijinta kuma zaa tambaye ta game da hakan. Bara ko yaron gida mai kiwo ne kan dukiyar mai gidansa, zaa kuma tambaye shi ta yadda ya gudanar da amanar kulawa da ita. Mai bada Hadisin yace, ina tsammani ya ce tabbas mutum mai kiwo ne kan dukiyar mahaifinsa Kuma za a tambayeshi game da hakan. Daga Littafin Sahih Bukhari.

5) SOYAYYA TSAKANIN MUMINAI

مُّحَمَّدٌ رَّسُولُ ٱللَّهِۚ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥٓ أَشِدَّآءُ عَلَى ٱلۡكُفَّارِ رُحَمَآءُ بَيۡنَهُمۡۖ تَرَىٰهُمۡ رُكَّعٗا سُجَّدٗا يَبۡتَغُونَ فَضۡلٗا
مِّنَ ٱللَّهِ وَرِضۡوَٰنٗاۖ سِيمَاهُمۡ فِي وُجُوهِهِم مِّنۡ أَثَرِ ٱلسُّجُودِۚ ذَٰلِكَ مَثَلُهُمۡ فِي ٱلتَّوۡرَىٰةِۚ وَمَثَلُهُمۡ فِي
ٱلۡإِنجِيلِ كَزَرۡعٍ أَخۡرَجَ شَطۡـَٔهُۥ فَـَٔازَرَهُۥ فَٱسۡتَغۡلَظَ فَٱسۡتَوَىٰ عَلَىٰ سُوقِهِۦ يُعۡجِبُ ٱلزُّرَّاعَ لِيَغِيظَ بِهِمُ
ٱلۡكُفَّارَۗ وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ مِنۡهُم مَّغۡفِرَةٗ وَأَجۡرًا عَظِيمَۢا

Muhammadu Manzon Allah ne. Kuma waɗannan da ke tãre da shi mãsu tsanani ne a kan kãfirai, mãsu rahama ne a tsakãninsu, kanã ganin su sunã

mãsu rukũ'i mãsu sujada, sunã nẽman falala* daga Ubangijinsu, da yardarSa. Alãmarsu tanã a cikin fuskõkinsu, daga kufan sujuda. Wannan shĩ ne siffarsu a cikin Attaura. Kuma siffarsu, a cikin Injĩla ita ce kamar tsiron shũka wanda ya fitar da rẽshensa, sa'an nan ya ƙarfafa shi, ya yi kauri, sa'an nan ya daidaita a kan ƙafãfunsa, yanã bãyar da sha'awa ga mãsu shũkar' dõmin (Allah) Ya fusãtar da kãfirai game da su. Kuma Allah Ya yi wa'adi ga waɗanda suka yi ĩmãni, kuma suka aikata ayyukan ƙwarai, daga cikinsu, da gãfara da ijãra mai girma. [Surah Al-Fatḥ: 29]

هَٰٓأَنتُمۡ هَٰٓؤُلَآءِ تُدۡعَوۡنَ لِتُنفِقُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ فَمِنكُم مَّن يَبۡخَلُۖ وَمَن يَبۡخَلۡ فَإِنَّمَا يَبۡخَلُ عَن نَّفۡسِهِۦۚ وَٱللَّهُ ٱلۡغَنِيُّ وَأَنتُمُ ٱلۡفُقَرَآءُۚ وَإِن تَتَوَلَّوۡاْ يَسۡتَبۡدِلۡ قَوۡمًا غَيۡرَكُمۡ ثُمَّ لَا يَكُونُوٓاْ أَمۡثَٰلَكُم

Ga ku, ya ku waɗannan! Anã kiran ku dõmin ku ciyar ga tafarkin Allah, sa'an nan daga cikinku akwai mai yin rõwa. Kuma wanda ke yin rõwa, to, yanã yin rõwar ne ga kansa. Kuma Allah ne wadãtacce alhãli kuwa kũ fãƙĩrai ne. Kuma idan kuka jũya (daga yi Masa ɗã'a), zai musanya waɗansu mutãne waɗansunku sa'an nan bã zã su kasance kwatankwacinku ba. [Surah Muḥammad: 38]

إِنَّمَا ٱلۡمُؤۡمِنُونَ إِخۡوَةٞ فَأَصۡلِحُواْ بَيۡنَ أَخَوَيۡكُمۡۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ لَعَلَّكُمۡ تُرۡحَمُونَ

Mũminai 'yan'uwan jũna kawai ne, sabõda haka ku yi sulhu a tsakãnin 'yan'uwanku biyu, kuma ku bi Allah da taƙawa tsammãninku, a yi muku rahama. [Surah Al-Ḥujurāt: 10]

لَّا خَيۡرَ فِي كَثِيرٖ مِّن نَّجۡوَىٰهُمۡ إِلَّا مَنۡ أَمَرَ بِصَدَقَةٍ أَوۡ مَعۡرُوفٍ أَوۡ إِصۡلَٰحِۭ بَيۡنَ ٱلنَّاسِۚ وَمَن يَفۡعَلۡ ذَٰلِكَ ٱبۡتِغَآءَ مَرۡضَاتِ ٱللَّهِ فَسَوۡفَ نُؤۡتِيهِ أَجۡرًا عَظِيمٗا

Bãbu wani alhẽri a cikin mãsu yawa daga gãnawarsu fãce wanda ya yi umurni da wata sadaka kõ kuwa wani alhẽri kõ kuwa gyãra a tsakãnin mutãne. Wanda

ya haka dõmin nẽman yardõdin Allah to za Mu bã shi lãda mai girma. [Surah An-Nisāʾ: 114]

Hadith

An karƀo daga Abu Hamzah, Anasin bin Malik RA hadimin Manzon Allah SAW, daga Manzon Allah SAW y ace: "Ɗayanku bai zamo mai Imani ba, har sai ya so ga ƈan uwansa abinda ya ke so a kansa na alkhairi". Bukhari da Muslim.

6) GUJEWA SHIRKA DA SAƁO

Jalla Jalaluhu cewa yayi:

يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَا تَتَّبِعُوا۟ خُطُوَٰتِ ٱلشَّيْطَـٰنِ ۚ وَمَن يَتَّبِعْ خُطُوَٰتِ ٱلشَّيْطَـٰنِ فَإِنَّهُۥ يَأْمُرُ بِٱلْفَحْشَآءِ وَٱلْمُنكَرِ ۚ وَلَوْلَا فَضْلُ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ وَرَحْمَتُهُۥ مَا زَكَىٰ مِنكُم مِّنْ أَحَدٍ أَبَدًا وَلَـٰكِنَّ ٱللَّهَ يُزَكِّى مَن يَشَآءُ ۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ

Ya ku waƈanda suka yi ĩmãni, kada ku bi hanyõyin Shaiƈan. Kuma wanda ke bin hanyõyin Shaiƈan, to, lalle ne shi, yanã umurni da yin alfãsha da abin da ba a sani ba (na Shirka da zalunci), kuma bã dõmin falalar Allah ba a kanku da rahamarSa, bãbu wani mutum daga gare ku da zai tsarkaka har abada, kuma amma Allah Yanã tsarkake wanda Yake so kuma Allah Mai ji ne, Masani. [Surah An-Nūr: 21]

حُنَفَآءَ لِلَّهِ غَيْرَ مُشْرِكِينَ بِهِۦ ۚ وَمَن يُشْرِكْ بِٱللَّهِ فَكَأَنَّمَا خَرَّ مِنَ ٱلسَّمَآءِ فَتَخْطَفُهُ ٱلطَّيْرُ أَوْ تَهْوِى بِهِ ٱلرِّيحُ فِى مَكَانٍ سَحِيقٍ

Kuna mãsu tsayuwa ga gaskiya dõmin Allah, ba masu yin shirka da Shi ba. Kuma wanda ya yi shirka da Allah, to, yanã kamar abin da ya fãƈo daga sama,

sa'an nan tsuntsãye su cafe shi, ko iska ta fãɗa da shi a cikin wani wuri mai nisa. [Surah Al-Ḥajj: 31]

وَمَن يَبْتَغِ غَيْرَ ٱلْإِسْلَٰمِ دِينًا فَلَن يُقْبَلَ مِنْهُ وَهُوَ فِى ٱلْـَٔاخِرَةِ مِنَ ٱلْخَٰسِرِينَ

Kuma wanda ya nẽmi wanin Musulunci ya zama addini, to, bã zã a karɓa daga gare shi ba. Kuma shi a Lãhira yana daga cikin mãsu hasãra. [Surah Āli-ʿImrān: 85]

MANYAN SABO:

Zina, Luwaɗi (namiji ya nemi namiji ta dubura, ko namiji ya nemi mace ta dubura), Maɗugo (mace ta nemi mace da jin daɗi kamar tana tare da namiji), Jima'i da dabba, Sata, Karya, Shaidar Zur, Kisan Kai, Shan Barasa (da ragowar kayan maye na ganye ko ƙwayar Bature), Rashin biyayya ga Mahaifa, Riya, Yi da mutane, Wulaƙanta Mutane, Girman Kai, Cin Mushe, Cin Naman Alade, Hassada, Giba, Kin aikata wajibi kamar Sallah akan lokacinta, ƙin yin Azumin Watan Ramadan da gangan, ƙin bayar da Zakka matuƙar akwai dukiyar, da sauransu, duk manyan zunubai ne. Amma duk da haka in ka tuba ko kika tuba da Zuciya ɗaya, watau tuban ɗanbaƙa, mutum ya gyara ya gabatar da aikin ƙwarai, kuma ya nemi gafarar Ubangijinsa, Allah zai karɓi Tubansa. Duba littafin Kaba'ir.

Shirka (haɗa wani da Allah cikin bauta), Kafirci (ƙin yarda da Musulunci ya zama shine Addinin mutum), su suka fi kuma manyan zunubai girma, domin duk wanda ya mutu yana cikin yi, to zai dauwama cikin Wutar Jahannama. Allah Ya kiyaye.

Sanarwa ita ce tamu, yarda ko ƙin yarda yana gareka, wannan kai ta shafa. Addu'ar mu ita ce Allah Ya sa mudace.

إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَغۡفِرُ أَن يُشۡرَكَ بِهِۦ وَيَغۡفِرُ مَا دُونَ ذَٰلِكَ لِمَن يَشَآءُۚ وَمَن يُشۡرِكۡ بِٱللَّهِ فَقَدِ ٱفۡتَرَىٰٓ إِثۡمًا عَظِيمًا }

Lalle ne, Allah ba Ya gãfarta a yi shirki game da Shi, kuma Yana gãfarta abin da yake bãyan wannan ga wanda Yake so, kuma wanda ya yi shirki da Allah, to, lalle ne ya ƙirƙiri zunubi mai girma. [Surah An-Nisāʾ: 48]

WASU DAGA CIKIN MANYAN HADISAN MANZON ALLAH SAW, DOMIN TARBIYYAR RUHI.

Sannan da faɗinsa Manzon Allah SAW (domin Allah Ya bashi "Jawami'ul kalimi" kalmomi taƙaitattu masu ɗauke da ɗunbun ma'ana), cikin Hadisansa:

1) Hadith. (Innamal a'amaalu binniyyaat.....)

An karɓo daga Abu Hafsin (Laƙabin Umar bin Khaɗɗaab, ana nufin baban Zaki saboda jaruntarsa), Umar ɗan Khaɗɗaab Allah Ya ƙara yadda a gareshi (RA) ya ce, ya ji Manzon Allah SAW ya ce "Da ɗai, ayyuka suna ɗamfare da niyyoyinsu ne, kuma lallai kowanne mutum akwai abinda yake fuskanta da niyyarsa, wanda hijirarsa ta kasance saboda Allah da ManzonSa ne (saboda Allah yayi kuma bisa koyi da koyarwar Manzon Allah SAW), to hijirarsa (ladan hijirarsa) tana ga Allah da ManzonSa (Allah ne Zai bashi lada saboda bin koyarwar Manzon Allah SAW), idan kuwa hijirarsa ta kasance ne domin wani abin duniya ko saboda mace da yake so ya aura, to hijirarsa tana ga wannan abinda ya niyyata (ba shi da lada gurin Allah AWJ)". Bukhari da Muslim suka rubuto. Wannan lafazin na Muslim ne tare da ƙarin bayanai na malamai cikin baka.

Karin bayani ga wannan Hadisi

Wannan yana nuni da cewar kafin kowanne aiki na Ibada ya zama na gari kuma karƃaƃƃe gurin Allah SWT, sai an Niyyace shi da hakan, kuma Niyyar ta kasance ta cika SHARUƊA UKU -

(1) (Niyyar) Bin Umarnin Allah na ka yi, ko ka bari.

(2) (Niyyar) Yi ko barin domin Allah Shi kaƈai ba tare da riya ba.

(3) (Niyyar) Koyi da Manzon Allah SAW cikin yin aikin.

Mu sani cewar Niyya a zuci take, kuma ba a furuci da ita a cikin dukkan aikin Ibada, sai cikin wasu aiyuka ƙidayayyu kamar lokacin aikin Hajji. Wannan haka a ka samu a Sunnar Fiyayyen Halitta SAW.

Watau duk wata Ibada sai ta sami Umarnin Allah na a yi ta, kuma sai an nufi Allah da ita Shi kaƈai, sannan anyi koyi da Manzon Allah SAW shi kaƈai cikin yin ta, take karƃaƃƃiya a gurin Allah, wadda Allah zai bayar da lada domin ta Duniya da Lahira. Duk wanda yayi aiki guda ƈaya mai kyau, yana da lada goma, daga bakin da baya ƙarya, watau bakin Manzon Allah SAW.

Amma kaga Ibadar da bata cika waƈannan Sharuƈa uku ba, to komai kyanta in har tana da shi, watsatstsiya ce gurin Allah AWJ. Ka yarda ko kar ka yarda wannan kai ta shafa. Misali karanta salatul fatih, karanta salatut Tananjina, Hizb Bahr, maulidin Annabi SAW, maulidin Tijjani da na Inyasi, ziyara ta ƙabarburan Waliyai da Shehunnai a Kano, Bauchi, Sakkwato da Kaulaha da sauransu. Duk waƈannan babu inda Allah ko ManzonSa suka yi umarni da yi, ko suka sami koyarwar Manzon Allah SAW.

2) Hadith. (Iz ɗala'a 'Alaina Rajulun.....)

An dai karbo daga Amirul Muuminin Umar dan Khaddab RA yace:

Wata rana muna zaune da Manzon Allah SAW, sai ga wani mutum ya zo mana, tufafinsa fari kal, gashin kansa baki wuluk, babu wata alamar tafiya tattare da shi (kai ka ce mazaunin gari ne wadda bai yi wata tafiya ba), kuma babu ɗaya daga cikinmu da ya sanshi. Sai ya tafi ya zauna gaban Manzon Allah SAW gwiwar sa na dungure da gwiwar Annabi, kuma ya ɗora tafukam hannayensa kan cinyoyinsa. Sai yace: Ya Muhammad faɗa mini menene Musulunci?

Manzon Allah SAW yace: Musulunci shine shaidawa babu abin bautawa da cancanta sai Allah Shi kaɗai, kuma Muhammad Manzon Allah ne, da tsayar da sallah, da bayar da zakka, da azumtar watan Ramadan, da hajjin ɗakin Allah ga wanda ya sami iko". Baƙon yace ka faɗi gaskiya. Sai muka yi mamakinsa domin yana tambayarsa kuma yana gasgata shi (watau dama ya san amsar tambayar kenan). Baƙon ya ci gaba da tamabaya ya ce: Bani bayanin menene Imani?

Manzon Allah SAW ya ce: Imani shine yin Imani da Allah da MalaikunSa da LittattafanSa da ManzanninSa da Ranar Lahira da kuma yin Imani da Ƙaddara mai kyau da marar kyau. Sai baƙon ya ce ka yi gaskiya. Ya sake tambayarsa: Bani labarin menene Ihsani (kyautata aiki)? Annabi ya ce: Ka bautawa Allah tamkar kana ganin Shi, domin in kai baka ganinShi to Shi Yana ganinka. Yace bani labarin lokacin Tashin Kiyama. Annabi yace ai mai tambaya bai fi wanda ake tambaya sani ba, (watau dukkansu basu san ranar ba. Sai ya ce to faɗa mini alamominta. Annabi ya ce baiwa ta haifi uwargijiyarta, sannan za ka ga marasa takalma, talakawa marasa isashen tufafi makiyaya suna tsere wajen gina dogwayen gidaje. Sai mutumin ya tashi ya juya ya tafi. Ni (Umar) kuma sai na ɗan saurara tare da Manzon Allah SAW. Sai Manzon Allah SAW y ace: Ya kai Umar, shin ka san mai tambayar can? Sai nace: Allah da ManzonSa ne

suka fi sani. Sai yace Jibrilu ne ya zo domin koya muku Addininku. Muslim ne ya rubuto.

Ƙarin bayani ga wannan Hadisi:

Wannan Hadisi ya tattara dukkan bayanai kan Addinin Musuluncin. Idan ka koma cikin Alƙur'ani za ka ga duk dalilai ga waɗannan bayanan. Idan ka bada gaskiya ka furta KALMA, sai yin IMANI, sai ayyuka na gaƀƀai, - SALLAH, AZUMI, ZAKKAH, HAJJI, sai kuma Kyautatawa cikin duk waɗannan ayyuka watau IHSAN.

Duka waɗannan ayyuka da Allah Ya yi Umarnin a aikata su, dole abi koyarwar Manzon Allah SAW cikin aikata su. Idan ka bi wani cikin aikata su ba Manzon Allah SAW ba, kayi aikin banza kuma kana da zunubi. Shi ya sa nake ganin wauta da rashin kan ƴan ƙur'aniyyun da Ƴan Tatsine, da suke rajin sai a daina aiki da Hadisan (SUNNAR) Manzon Allah SAW (Koyarwarsa ga wannan Addini) da ta zo cikin Littattafan Hadisi irin su Sahihul Bukhari, Sahihu Muslim da sauransu. Wannan ba ƙaramar damƙewar basira ce ba. Waɗancan mutane sun yi watsi da karantarwar Malam mai ahallari. Inda yace "ka yi koyi da malamai masu riƙo da SUNNAR Manzon Allah SAW). Idan baka karanta hadisi ba ta yaya zaka san SUNNAR Manzo? Allah Ya sauwaƙe Ya raba mu da ƙaramin sani wanda masu magana suka ce ƙuƙumi ne.

3) Hadith. (Man hadatha fi amrina.....)

Hadithi daga Uwar Muminai babar Abdullahi A'ishatu (matar Manzon Allah (SAW)) tace, Manzon Allah (SAW) ya ce "Duk wanda ya ƙirƙiri wani sabon abu a cikin wannan al'amarin namu (na Addini), wanda tun asali babu shi ciki to maidajje ne zuwa gareshi (baza a karƀa ba a matsayin Addini)". Bukhari da Muslim kuma hadithi na 5 cikin Arba'una Ahadith.

Ƙarin bayani ga wannan Hadisi:

Wannan kuwa ƙarara yake domin ya saƃawa ƙa'idojin aiki mai sunan "Aiki na gari karƃaƃƃe gurin Allah SWT", kamar yadda aka yi bayani nan sama kaɗan. Saboda kuma an riga an KAMMALA MANA WANNAN ADDINI tun Hajjin ban kwana, ranar Tsayuwar Arafah shekara ta goma da Hijrar Manzon Allah SAW daga Makka zuwa Madina. Ƴan bidi'a kun shiga uku, ku tuba ku dawo ga Addinin Musulunci, Sunnah Sak - Bidi'a Sam.

4) Hadith. (Innal halala baiyinun.....)

An karbo daga Abu Abdullahi An-Nu'man dan Bashir RA yace ya ji Manzon Allah SAW yace: "Lallai Halal a baiyane ta ke kuma Haramun ma a baiyane ta ke, kuma tsakaninsu akwai al'amura masu rikitarwa waɗanda da yawa daga cikin mutane basu sansu ba. Duk wanda ya kaucewa rikirkitattun abubuwa, ya tserar da Addininsa da kuma mutuncinsa. Wanda ya abka cikinsu kuwa to ya abka cikin Haram. Kamar mai kiyon dabbobi gefen shinge, bai aune ba sai dabbobinsa su abka cikin shingen. Ku saurara, lallai ga kowanne sarki akwai iyaka (ta mulkinsa), ku saurara, lallai iyakar Allah ita ce duk abinda Ya haramta. Ku saurara, tabbas a cikin jiki akwai wata tsoka, idan ta gyaru dukkan jiki ya gyaru, idan ta ƃaci dukkan jiki ya ƃaci, ku saurara, ita ce ZUCIYA. Bukhari da Muslim.

Ƙarin bayani ga wannan Hadisi:

Bayan Umarni da Allah Ya yi domin yin aiki ga bauta maSa, sai kuma Hani da cewa kada a aikata wasu abubuwa masu cutarwa ga ɗan Adam, domin Allah babu wanda ya isa ya cutar da Shi da komai.

Waɗannan Halal da Haram duk Allah Ya baiyana su cikin Alƙur'ani mai Tsarki, sannan Sunnar Fiyayyen Halitta SAW ta ƙara haske a kai.

Tun wancan lokacin Manzon Allah SAW ya ce akwai rikirkitattun abubuwa ballantana yanzu da shaiɗanci ya ƙaru saboda tafiyar zamani, Allah Shine mai zamani. Jan kunnen shine ka gujewa duk wani rikirkitaccen al'amari domin ka zauna lafiya.

Misalin rikirkitattun abubuwa a wannan zamani sune kamar "Forex Trading" duba Littafi na mai suna "Daidai da Rashin Daidai kan Hadadar Kuɗaɗen Waje", da wani nau'i na mu'amalar ma'aurata na 69.

Wani sashi na Forex trading caca ce a ƙudundune. Shi kuwa mu'amalar ma'aurata ta 69 (kai da ƙafa), ta yadda shi zai ringa tanɗa da tsotson kan hancin butar ta (tsududu butar Allah, kanki na ƙasa ba kya zubda ruwa, cikinki damuna bayanki yabanya), ita kuma tana tanɗa da tsotson ɗan yatsarsa na wajen aljihun wando, ba ya cikin ɗabi'ar da Allah ya halicci mutum a kai. Sannan kalle-kallen fina-finai na fasiƙanci (blue Film) daga waɗanda ba Musulmai ba, shi ya haifar da duk irin wannan halaiyar cikin Musulmai.

Mahaɗin turmi sai taɓarya. Ko ɗan akuya sunsunawa kawai yake yi, sannan ya ci gaba da aiki. Duk da cewa ba inda aka ce halal ne ko haram ne, to gujewa wannan halaiyar shi ya fi kyau. Sannan wata matar, tana buɗe cinyoyinta, ɗoyin ruɓaɓɓen kifi ne kawai zai bugi hanci ka. Saboda haka, ko kafi ɗan akuya da kare da zomo jaraba, ka haƙura da kai hacinka wajen. Allah Ya sauwaƙe.

Sannan mu sani cewar Manzon Allah SAW ya ce "Allah Ya la'anci duk mai kallon tsiraicin wani, sannan Allah Ya la'anci wanda ya bari ake ganin tsiraicinsa". Wannan kuwa ko a hoto ne marar motsi ballanta mai motsi da za a bijiro maka da komai tawai, ta yadda baka tsammani. Allah Ya gafarta mana.

Amma wannan haramci na ganin tsiraicin wani, bai shafi ma'aurata biyu a junansu ba, ko abinda mutum ya mallaka na bayi mata, waɗanda bai aurar da su ga wani ba (idan har yanzu da akwai).

5) Hadith (Ya gulaam inni u'allimuka kalimaat……...)

An karɓo daga Baban Abbas, Abdullahi ɗan Abbas RAm ya ce: Wata rana ina bayan Manzon Allah SAW akan abar hawarsa sai ya ce mini: "Ya kai wannan yaro, lallai zan sanar da kai wasu kalmomi; ka kiyaye Allah sai Ya baka kariya, ka kiyaye Allah sai ka same Shi gaba gareka, idan za ka yi roƙo, to roƙi Allah (Shi kaɗai), idan za ka nemi taimako, to nemi taimakon Allah Shi kaɗai, ka sani cewar, da duk al'umma za su taru domin su amfaneka da wani abu, to ba za su amfana maka da komai ba, face abinda Allah SWT Ya riga Ya ƙaddara maka. Da kuma za su taru domin su cutar da kai da wani abu, to ba za su iya ba, face da abinda Allah Ya ƙaddara maka tun farko. An ɗage alƙalami, takardu sun bushe. TirmidhYai ya rubuto.

Ƙarin bayani:

Wannan Hadithi yana nuni kan cewa lallai in ka kiyaye Allah cikin mu'amalarka da Shi da kuma ragowar bayinSa to lallai zai baka kariya ta ko'ina. Kiyaye Allah shine kiyaye dokokinSa na Umarni da Hani, a ɓoye da sarari. Wannan shi zai ƙara maka TAƘWA.

Abu na biyu shine, ba a roƙon kowa (cikin abinda Allah ne kawai zai iya yi, kamar samun haihuwa, lafiya, arziki da sauransu), ko Neman taimakon agajin gaggawa (kamar neman kariya daga faruwar wani mummunan abu da ake ganin gashinan gadan-gadan zai auku) ga kowa , sai Allah Shi kaɗai. Da wannan ne TAUHIDIN mutum yake daɗa ƙarfafuwa a cikin zuiyarsa. Yin wannan ga wanin Allah shi ake cewa SHIRKA. Ka yarda ko kar ka yarda wannan kai ta shafa.

Abu na uku shine, koya maka yin imani da ƙADDARA mai kyau da maras kyau. Tun ran gini ran zane in ji Bahaushe. Allahu Akbar kaji makarantar Manzon Allah SAW wadda waɗansu zindiƙai suke inkari.

6) Hadith. (Man kazaba 'alaiya.....)

An karɓo daga Rib'iyi bin Hisham cewa ya ji Sayyiduna Aliyu RA cikin wata khuɗuba da ya ke bayarwa yace: Manzon Allah SAW ya ce "Kada ku faɗi ƙarya game da Ni, domin duk wanda ya faɗi ƙarya game da Ni zai shiga Wuta. Muslim ne ya rubuto.

Ƙarin bayani.

Allahu Akbar malam kaji koyarwar Fiyayyen Halitta. Ta yadda ya ɗaure kuma ya tsare Addinin Musulunci. Wannan shi ake kira da AMANAR ILIMI, ka bayar da shi yadda yake, babu ragi, babu ƙari. SAW.

Duk wanda ya ce Annabi ya ce kaza-da-kaza, alhali Annabin bai faɗa ba, to ya shiga uku, Wutar Jahannama ɗoɗar babu kwana babu taka burki.

Haka kuma, duk wanda Annabi ya riga ya faɗi kaza-da-kaza, amma ya ƙaryata, yace a'a Annabin bai ce kaza-da-kaza ɗin ba, To shima ya yiwa Annabin Rahma ƙarya, kuma Wutar Jahannama ita ce makomarsa ɗoɗar babu kwana babu jan burki.

Musussuka da ragowar ɣan ƙala ƙato masu ƙaramin sani ƙuƙumi ne da Sufaye (masu cewa Annabi ya basu wata Ibada a mafarki ko a baiyane ƙarara ko Masu da'awar wani Fathi (Ilhama ko Wahayi)) ina aka kwana? Allah Ya sauwaƙe.

Saboda haka Addinin Musulunci tuni yake a ƙaiyade. Babu ragi babu daɗi. Duk wanda zai yi magana kan Addinin Musulunci ya ji tsoron Allah, hujjarsa ta zama daga cikin Alƙur'ani da Sunnar Manzon Allah SAW. Idan babu stampi da goyon

bayan Alƙur'ani ko Sunnar Fiyayyen Halitta, to Kasan cewar wannan abin "kitabur Ra'asi" ne watau molon ka ne kawai. Ya Allah! muna neman shiriya daga gareKa zuwa ga Hanya Madaidaiciya, da kariya daga faɗawa cikin hanyar da wasu mutane ke bi ta molon ka, babu Ayar Alƙur'ani babu Hadisin Manzon Allah SAW.

7) Hadith (Daga cikin khuɗubatul wada'i, khuɗubar ban kwana, lokacin Hajjin bankwana na Manzon Allah SAW cikin shekara ta 10 da hijrah)..

Game da haramta jinnin fansa na lokacin faɗace-faɗacen Jahiliyya, cin riba, da umarni da kulawa da mata da umarni da riko da Kitab (Alƙur'ani).

An karbo daga Ja'far bin Muhammad wanda yace: Babanshi yace: Mun je wajen Ja'afar bin Abdullahi sai yake tambayar waɗanda suka je domin ganin shi, har sai da zagaye ya zo kai na. Na ce nine Muhammad bin Ali bin Husain RA. Na ce masa fada mini game da Hajjin Manzon Allah SAW. Sai ya yi alama ga tara da hannunsa (watau ranar tsayuwar Arafah) sannan yace: Manzon Allah SAW ya zo ƙasan dutsen ya yiwa mutane khuɗuba da cewar:

"Hakika jininku, dukiyarku sun haramta kamar yadda wannan ranar taku take haramun, cikin wannan wata naku, a cikin wannan gari naku. Ku sani, duk wani abu na Jahiliyya na take shi ƙarƙashin ƙafata, ya zama Haramun (daga yau ɗin nan kuma a yanzu nan). Haramun shine ɗaukar jinin fansa na lokacin Jahiliyya. Jini na fansa da muke bi wanda shine farkon wanda aka Haramta shine na ɗan Rabi'a bin Harith, wanda aka raine shi a cikin ƙabilar Sa'ad kuma Hudhail suka kashe shi. Haka Ribar Jahiliyya an sauke ta, kuma farkon ribarmu dana sauke ita ce ta 'Abbas bin 'Abdulmuɗɗalib. Ku ji tsoron Allah game da matanku. Hakika kun ɗauke su ne cikin kariyar Allah SWT, kuma jima'i (tarawa) da su halas ne da kalmomin Allah (Halaccin a cikin Alƙur'ani yake). Kuna da hakki a kansu na cewar kada su bar wani ya shiga gidajenku matuƙar baku aminta ba. Idan sun yi haka to ku tsawatar (doke su) musu amma tsawatarwa maras

cutarwa. Su kuma hakkin su a kanku shine na ku basu abinci ku tufatar da su gwagwadon hali. Zan tafi (ma'ana zan rasu) in bari a tsakinku Littafin Allah, kuma idan kuka yi riko da shi, ba za ku taɓa ɓata ba. Kuma za a tambayeku game da ni (a Ranar Lahira), (ku faɗa mini) me za ku ce game da Ni? Duk jama'ar gurin suka ce: za mu bayar da shaidar cewa ka isar da sako ka aiwatar da Annabcinka kuma ka bayar da nasiha da jagoranci na gari. Mai bayar da labarin ya ce: sai Manzon Allah SAW ya ɗaga ɗan yatsarsa manuniya sama, sannan ya yi nuni ta ita (ɗan yatsar) ga jama'a yace musu: "Ya Allah ka shaida", "Ya Allah Ka shaida", har sau uku. Sahih Bukhari

Game da haramta riba.

3334. An karɓo daga Sulaiman bin 'Amr, cewar babansa ya ce: "Na ji Manzon Allah SAW, lokacin Hajjin bankwana, ya ce: 'Duk Riba da ta samo asali daga jahiliyya an soke ta; kuna da uwar dukiyarku. Kada kuyi mu'amala ta rashin adalci, haka kada a yi muku mu'amala ta rashin adalci. Duk wani jini da ake bi na bashin faɗan ƙabilanci tun lokacin jahiliyya an soke shi, kuma jinin farko da na soke shine na Al-Harith bin 'Abdul-Muttalib wanda Banu Laith suka raine shi kuma Hudhail suka kashe shi.' Manzon Allah ya ce: 'Ya Allah, na isar (da saƙon)?' kuma suka ce (Sahabbai): 'Na'am' - sau uku. Ya ce SAW: "Ya Allah, Ka shaida!' har sau uku." (Hasan). Bukhari..

Game da biyan bashi

1265. Abu Umamah ya ce: "Lokacin Hajjin bankwana, Na ji Manzon Allah SAW yana cewa lokacin khuɗuba: 'Abinda aka ranta (ko aka ara) lallai a biya (ko mayar da shi), kuma mai lamuni shine da ɗaukar nauyi, kuma dai bashi dole a biya." (Hasan) At-Tirmid

Game da haramcin Jini, Dukiya, Mutunci da ɗaukar laifi.

2159. Sulaimãn bin 'Amr bin Al-Ahwas ya hakaito daga babansa wanda ya ce: "Lokacin Hajjin bankwana, Na ji Manzon Allah SAW yana cewa: 'Wacce rana ce wannan?' Suka ce: 'Ranar Hajjin Babbar Sallah ce. Ya ce: 'Lallai Jininku da dukiyarku da mutuncinsu Haramcin ne ga kowannen ku, kamar yadda wannan Rana taku take Haramun a cikin wannan gari naku. Lallai, babu wani da zai ta'addanci (ko zalunci) face alhakin abin yana kan shi. Lallai babu wani (uba) da zai yi ta'addanci kuma a riƙi ɗan sa da laifin. Haka ɗa ba zai yi laifi ba a kama ubansa da laifin. Tabbas Ash-Shaiɗan ya fidda tsammanin za a bauta masa har abada a cikin wannan gari naku. AtTirmidhi.

3055. An karƀo daga Sulaiman bin 'Amr bin Ahwas cewa babansa ya ce " Na ji Manzon Allah SAW lokacin Hajjinsa na bankwana, ya ce: "Ya mutane na, wacce rana ce mafi Haramtuwa sau uku? Su ka ce, Ranar Babbar Hajji. Ya ce, Jininku da dukiyarku da mutuncinku Haramun ne kan kowannen ku kamar yadda wannan ranar taku take Haramun, a cikin wannan wata naku a cikin wannan ƙasa taku. Babu wani mai yin zunubi da zai aikata wani zunubi face alhakin zunubin yana kansa. Babu wani mutum da za a hora saboda zunubin mahaifinsa. Shaiɗan ya fidda tsammanin za a bauta masa har abada a wannan ƙasa taku. Amma za a yi masa biyayya kan ƙananan abubuwa marassa muhimmanci kuma zai wadatu da wannan kawai. Duk wani bashin Jini na faɗan ƙabilanci an soke shi (daga yau), kuma jinin farko da na soke shine na Harith bin Abdulmuɗalib, wanda aka raine shi cikin ƙabilar Laith kuma Hudhail ya kashe shi. Duk wata riba ta jahiliyya an soke, amma kuna da uwar kuɗin ku. Kada ku cutar da wani, babu wanda zai cutar da ku. Ya al'ummata shin na isar da Manzanci? Ya tambayi wannan sau uku. Sai suka ce "E", sai ya ce "Ya Allah Ka shaida" har sau uku. Hadithi Hasan. Sunan Ibn Majah.

8) Hadith (Za a Rarraba a zama ƙungiya-ƙungiya har 73)

Duk da Allah SWT Ya ja kunnen Musulmai da kada su rarraba cikin Ayoyin Alkur'ani, amma cikin IliminSa SWT Ya san sai an rarrabu, shi ya sanya ya tsinkayar da AnnnabinSa domin daɗa ja mana kunne.

Hadithi daga baban Amir al Auzani cewar Mu'awiyya ɗan Abu Sufyan ya tsaya cikinmu yace "Manzon Allah (SAW) ya tsaya cikinmu yace "mutanen da suka gabaceku mazowa littafi (Yahudu da 'Yan Mishan) sun karkasu kashi saba'in da biyu, kuma wannan al'umma (Musulmai) zasu karkasu saba'in da uku, waɗanda saba'in da biyu daga cikinsu duk Wutã zasu shiga, kaso ɗaya ne 'Yan Aljanna. Sune waɗanda basu rarraba ba suke tare da Jama'a. Ibn Yahya da Amr sun ƙara cikin hadithinsu cewar "waɗansu mutane za su bayyana cikin wannan al'ummar tawa, son zuciya da son Jin daɗin duniya zai lulluɓe su, kamar yadda cutar mahaukacin kare wadda bata barin wata jijiya ko ƙashi na maras lafiya face sai ta shigeta"". Sahih daga sunan Abu Dawud.

Karin bayani ga wannan Hadithi

Lallai tabbas, wannan magana ta cikin wannan Hadithi tabbatacciya ce duba ga irin ɗariƙoƙin sufaye da suka baiyana cikin ƙasashen Musulmai a yau a kan doron ƙasar nan. Duk ƙasar da ka je sai ka sami wasu ɗariƙun ɓata da Shehunnai suka ƙirƙirowa kansu da Jahilan mabiyansu wani sabon addini da babu ƙalal-Lahu, babu ƙala Rasulul-Lah sai molon ka.

9) Hadith (Karshen Zamani, alamomin Tashin Kiyama).

80. Anas RA ya ce, Manzon Allah SAW ya ce: "Yana daga alamun Tashin Kiyama waɗannan abubuwa:1) Za a ɗauke Ilimin Addinin Musulunci (ta hanyar mutuwar ƙwararrun masu ilimin Addinin.

2) Jahilci (kan Addinin) zai tabbata

3) Shan barasa (giya) zai yawaita (zai zama ba sabon abu ba ne)

4) Zina za ta baiyana a fili. Sahih Bukhari

81. An karƀo daga Anas RA ya ce: Zan faɗa muku wani hadisi wanda babu mai faɗa muku shi bayan Ni. Na ji Manzon Allah SAW yana cewa: "Gabatowar Tashin Ƙiyama akwai waɗannan abubuwa":

1) Ilimi (na Addini) zai yi ƙaranci

2) Jahilci zai yaɗu (ya zama ado)

3) Za a sami yawaitar baiyanar zinace-zinace a fili

4) Mata za su yawaita, maza za su yi ƙaranci ta yadda mata hamsin za su zama cikin ƙarƙashin kulawar mutum namiji ɗaya. Sahih Bukhari.

Komai taƀarƀarewar zamani sai an sami masu bin asalin Musulunci na Gaske ba jabu mai cushe-cushe ba.

372] 232 - (145) An karƀo daga Abu Huraira wanda ya ce, "Manzon Allah SAW ya ce "Musulunci ya fara yana mai baƙo, kuma zai koma (a ƙarshen zamani) yana baƙo, saboda haka kyakkyawan Albishir ga baƙi". Sahih Muslim

374] 233 - (147) An karƀo daga Abu Huraira cewa, Manzon Allah SAW ya ce "Imani zai tattare ya koma Madina kamar yadda maciji yake tattarewa ya koma cikin raminsa". Sahih Muslim

10) Umarnin Isar da Saƙon Manzon Allah SAW

Sannan Manzon Allah SAW ya ce a isar daga gareshi watau a sanar da al'umma wannan Addini kamar yadda yake daga gurin shi SAW.

عن عبد الله بن عمرو قال :قال رسول الله صلّى الله عليه وسلم بلغوا عني و لو آية

An karƀo daga 'Abdullahi bin 'Amr ya ce: Manzon Allah SAW ya ce "Ku isar daga gareni koda aya ɗaya ce". Daga Littafin Musnad Ashshihaab Mujalladi na ɗaya shafi na 387 Hadithi na 662.

Bayan wannan, ya ja kunnen al'umma da ɗai kada wani ya kuskura ya jingina masa ƙarya:

An karƀo daga Rib'iyi bin Hisham cewa ya ji Sayyiduna Aliyu RA cikin wata khuɗuba da ya ke bayarwa yace: Manzon Allah SAW ya ce "Kada ku faɗi ƙarya game da Ni, domin duk wanda ya faɗi ƙarya game da Ni zai shiga Wuta. Muslim ne ya rubuto.

An karƀo daga Abu Huraira RA ya ce : Manzon Allah SAW ya ce "Duk wanda ya yi mini ƙarya da gangan, ya tanadi wajen zamansa a Wuta". Muslim ne ya rubuto.

Wajejen ƙarshen rayuwarsa a doron ƙasar nan Manzon Allah SAW ya yiwa Sahabbansa babbar Nasiha:

11) Hadith (Nasihar Bankwana)

Hadithi daga baban Najihin Irbaɗi dan Sa'ariyata Allah Ya ƙara yadda a gareshi ya ce: Manzon Allah (SAW) ya wa'azantar damu da wani wa'azi mai girgiza zukata, kuma idanuwa suka kwaranyar da hawaye. Sai muka ce Ya RasululLahi wannan kamar wa'azin mai ban kwana (da duniya), to i mana wasiyya. Yace ina yi muku wasiyya da kuji tsoron Allah Mabuwayi Maɗaukaki, sannan ku ji, ku yi biyayya ga koda bawa ne aka shugabantar a kanku. Saboda duk wanda yayi tsahon rayuwa a cikinku zai ga saƀani da yawa (cikin wannan Addini), to na horeku da bin Sunnata da Sunnar Shiryayyun Khalifofi masu shiryarwa (Abubakar, Umar, Uthman da Aliyu, Allah Ya ƙara yadda da su). Ku yi riƙo gam-gam da fiƙoƙinku (ga waɗannan Sunnoni), sannan na hane ku da

bin ƙirƙirarrun abubuwa, domin Lallai dukkan wani ƙirƙirarren abu ɓata ne". Dawud da Timidhi suka rubuto.

12) Hadithi (Rasuwarsa, SAW)

3536. An karɓo daga Uwar Muminai A'ishatu RA, Matar Manzon Allah SAW ta ce: Manzon Allah SAW ya rasu yana da shekaru sittin da shida. Bukhari

6509. An karɓo daga Uwar Muminai A'ishatu RA, Matar Manzon Allah SAW ta ce: Lokacin da Manzon Allah SAW yake cikin ƙoshin lafiya yakan ce: " Babu wani rai na Annabi da za a karɓa (rasuwa) face an nuna masa gidansa a Aljannah sannan a bashi zaɓin mutuwa ko rayuwa". Saboda haka lokacin da ya zo rasuwa SAW, kansa yana kan cinyata sai hankalinsa ya gushe (ya suma) na ɗan wani lokaci, sai kuma ya farfaɗo tare da ƙura idanuwansa ga rufin ɗaki, ya ce: "Ya Allah (tare) da maɗaukakin aboki". Sai na ce, "Kenan bai zaɓi ya zauna da mu ba, (watau ya zaɓi ya rasu tun da an nuna masa gidansa na Aljanna)". Sai na fahimta cewar wannan shine tabbatuwar Hadisin da shi Annabin ya ringa faɗa mana. Kuma wannan shine ƙarshen abinda Annabi yayi furuci da shi kafin rasuwarsa SAW " Allahumma Rafiƙal 'A'alaa". Duba Ƙur'an Sura ta 4 aya ta 69. Sahih Bukhari

وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَٱلرَّسُولَ فَأُوْلَـٰٓئِكَ مَعَ ٱلَّذِينَ أَنْعَمَ ٱللَّهُ عَلَيْهِم مِّنَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ وَٱلصِّدِّيقِينَ وَٱلشُّهَدَآءِ وَٱلصَّـٰلِحِينَۚ وَحَسُنَ أُوْلَـٰٓئِكَ رَفِيقًا

Kuma waɗannan da suka yi ɗã'a ga Allah da Mazonsa, to, waɗannan sunã tãre da waɗanda Allah Ya yi ni'ima a kansu, daga annabãwa da mãsu yawan gaskatãwa, da masu shahãda da sãlihai. kuma waɗannan sun kyautatu ga zama abõkan tafiya. [Surah An-Nisāʾ: 69]

Allahu Akbar, Allahu Akbar, Allahu Akbar. Innaa lilLahi wa innaa ilaiHi raajiuun. Ya Allah Ka ƙara daɗin Salati da Tsira da Aminci ga AnnabinKa kuma ManzonKa Annabin Rahma, Muhammad ɗan 'AbdulLahi da Sahabbansa da

Iyalansa baki ɗaya da ma ragowar Musulman da ke kan Hanya irin tasu har ya zuwa Ranar Tashin Ƙiyama.

A DUNƘULE

Wannan shine taƙaitaccen bayani kan Annabi Muhammad da Addinin Musulunci tare da duk wani gargaɗi da busharar da Allah Ya yiwa Muminai da kuma narkon dake jiran Kafirai Ranar Ƙiyama. Wannan shine Addinin da Annabi SAW ya koyawa Sahabbansa da Matansa da Ƴayansa, kuma suka rayu akai, suka rasu a kai suka koma ga Maliccinsu. Daga cikin Sunnar Manzon Allah SAW, wadda take fassara Alkur'ani aka fitar da SHARI'A da FIQHU waɗanda sune babban jigo cikin aikace-aikacen ADDININ MUSULUNCI, kuma duk wannan a ZAHIRI yake ba a ɓoye ba.

Babu wani abu a ɓoye game da Addini wanda Annabi SAW bai koyawa Sahabbansa ba lokacin da yake a raye tare da su. Alƙur'ani a rubuce yake a baiyane, Sunnar Annabi a rubuce take a baiyane. Wanda ya sani, ya sani, wanda bai sani ba, sai ya koma MAKARANTA.

Babban Ginshikin koyarwar Addinin Musulunci wadda ya zo a cikin Babban Ginshikin Littafin Musulunci watau Alkur'ani, shine TAUHIDI. Domin a Bautawa Allah Shi kaɗai, ba tare da haɗa Shi da wani cikin bautar ba, watau Shirka. Duk Manzanni da suka gabaci Annabi SAW, abinda Allah AWJ Ya aiko su akai kenan. Duk waɗannan bayanan, suna cikin hasken Nassosin Alƙur'ani mai Tsarki tare da fashin baƙin Fiyayyen Halitta cikin Sunnarsa wadda a ka rubuce cikin littattafan hadisai daban-daban.

Sanin TAUHIDI tsantsa (Allah ne kaɗai Mahaliccin kowa da komai, Mai arzuta kowa da komai da ni'imoninSa, kuma Shi kaɗai Ya cancanci a Bauta masa. Sa'annan kowa da komai bawa ne ga Allah kuma dole bawa ya bautawa Allah

Shi kaɗai ba tare da shirka ba), shi ke sanya mutum Wadatar zuci da Tawadi'u da Zuhdu. Waɗannan su suke ƙarawa Zuciya Taƙwa, da Ikhlasi cikin aiyukan Ibada tare da Kyautatawa. Muna roƙon ALLAH SWT Taufiƙi.

Sannan babu wani rubutaccen ilimi na Baɗini daga Manzon Allah SAW ko daga Sahabbansa. Kuma duk wanda ya ce Annabi ya taso daga ƙabari ya ba shi wani abu na addini, ya yiwa Allah da ManzonSa ƙarya kuma abin a titsiye shi ne ya kawo hujja. In ya kasa ko dai ayi masa nasiha ya janye ya koma ga Sunnah, ko in ya ƙi a fille masa kai domin ya daina kawowa Musulmai ruɗu cikin Addinin su.

RIKICI CIKIN ADDININ MUSULUNCI DA WASU SUKA HAIFAR.

Duk da Jajircewar da Sahabbai suka yi da Tabi'ai da Tabi'ut-Taabi'ina da Salihan bayi cikin wannan Tawaga ta Fiyayyen Halitta, domin ganin wannan Addini ya sami kariya domin kaiwa ga na ƙarshen zamani lafiya-lafiya, sai da aka samu wasu masu son ZUCIYA da suka yi cushe cikin Musulunci ta hanyar ƙirƙiro ɗariƙun ƃata suka gurƃata tafiyarsa. Kamar yadda aka samu a Yahudanci da Kiristanci.

Koda yake tun lokacin da Manzon Allah SAW yake raye aka fara samun masu da'awar Annabta irin su Musailamah al-Kazzaab domin rikirkita Addinin Musulunci.

Musailimah (Musulmai ne suka ƙanƙastar da sunansa na asali ya koma Musailimah) wanda cikakken sunansa shine Maslamah ibn Habib al Hanafi, ɗan ƙabilar Hanafi wadda ɗaya ce daga cikin manyan ƙabilun larabawa, ya yi da'awar Annabta, ta yadda ya rubutawa Manzon Allah SAW cewa:

Daga Maslamah Manzon Allah zuwa ga Muhammad Manzon Allah, aminci ya tabbata a gareka. Ka sani cewa an bani wani kaso daga cikin wannan al'amari (na Addinin Musulunci), saboda haka, rabin duniya ta mu ce (mu ƙabilar Hanafi), rabin duniya kuma ta Quraishawa (Ƙabilar Manzo Allah SAW), Amma su Quraishawa sun wuce gona da iri (sun keta haddin Allah).

Sai Manzon Allah Muhammad SAW ya mayar masa da amsa kamar haka:

Daga Muhammad Manzon Allah (SAW) zuwa Musailimah al-Kazzaab (mugun maƙaryaci), Aminci ya tabbata ga wanda ya bi Shiriyar Allah, bayan haka, haƙiƙa ƙasa (duniya) ta Allah ce kuma Yana bayar da ita, ga duk wanda Ya ke so cikin bayinSa. Kuma ƙarshen (sakamakon al'amari mai kyau) yana ga masu Taƙwa (tsoron Allah na haƙiƙa).

Bayan rasuwar Manzon Allah SAW, Musulmai ƙarƙashin khalifancin Abubakar As-Siddiƙ bisa jagorancin kwamandan Sojojin Musulmai, Khalid bin Walid suka yi fata-fata da rundunar Maƙaryaci Musailamah, aka ƙarar da su, Musuluncin na Gaske ya ci gaba da wanzuwa.

Munafukai ba su bar Musulunci da Musulmai sun zauna lafiya ba. Har abinda ya faru cikin Musulmai ya faru, bayan rasuwar Khalifa Umarul Farouƙ. Daga nan aka fara samun ƊangarorI-ƊangarorI cikin Addinin Musulunci.

Ɗariƙoƙin Shi'a da na Sufaye da sauransu kamar Ahmadiyya sun taka rawa ƙwarai wajen rarraba kan Musulmai tare da gurɓata Aƙidun Musulunci na Asali, musamman cikin TAUHIDI da cikin Ƙaunar Sahabbai da Matan Manzo. Su Sahabban nan da Matan Manzo su suka koyo wannan Addini daga Manzon Allah SAW, suka koyar da Tabi'ai, su kuma suka koyar da na bayansu har zuwa kanmu.

Kamar yadda Yahudanci da Kiristanci suka Kambama Annabawan su, har suke ganin ɣaɣan Allah ne, kokuwa suma sun zama Allah, to haka wasu ɗariƙun Sufaye suke Kambama Shehunansu har suna cewa sun fi Allah. Waiya zubillahi. Duba littafina mai suna "Musulunci da Sufanci a Ifriƙiyya". Kaɗan daga ciki shine kamar haka:

GINSHIƘAN SUFANCI:

1) Tsoron Allah da gudun duniya (suna riyawar hakan). Saboda a hankali za ka fahimci ƙarya su ke yi.

2) Keɓancewa (shiga halwa) domin tunani da Zikri. Zikirin da suka ƙirƙiro tare da kaifiyyar yin sa, cikin masallatai da zaawiyyarsu. Ana rawa da kade-kade har da tsalle da majajjawa wasu lokutan.

3) Ƙirƙira ko Jingina da wata ɗariƙa domin saduwa da Muƙaddami (dole wani muƙaddami yayi maka tsani, kuma dole sai ta hanyar Ɗariƙa).

4) Yarda da bin wasu aikin ibada sabi waɗanda Waliyin ko Shehun ɗariƙar ya ƙago, ɗoriya kan koyarwar Manzon Allah SAW.

5) Yarda da ziyarar maƙabartu tare dayin bauta ciki ga Shehunnai da Waliyyai. (Wannan shirka ce)

6) Yarda da cewar Annabawa da Waliyai da Shehunnai ke juya akalar duniya na arzutawa da talautawa. Duk abinda kake da shi na arziki ko lafiya ko yaya, to Shehi ne ko Wali ko Annabi ya baka, ba Allah ba. (Ƙarya ce, Allah ne kawai Mai arzutawa Mai talautawa Mai rayawa Mai kashewa).

7) Yarda da cewar Wali ko Annabi zai iya tashi bayan ya mutu har ya bayar da wata ibada. (Wannan ƙarya ce. Kullu nafsin zaa'iƙatul maut). Ina jin dai kasan mecece mutuwa koda baka mutu ba a yanzu.

8) Yarda da ƙarerayi waɗanda babu hujja ko ƙanƙani a kai. Ƙarerayin da basu sami goyon bayan Alƙur'ani ko Hadisan Manzon Allah SAW ba.

9) Hana Tambayar dalili ko hujja ga Shehu ko Wali, akan duk abinda ya aikata ko ya umarci muridi da ya aikata. Kuma dole ka kasance kamar gawa gaban mai wanke ta duk lokacin da ka je gaban Shehi ko wani Wali.

10) Barrantuwa da duk wata ɗariƙa da Shehun ɗarikar da ba ta mutum ba. Watau duk wata ɗariƙa tare da Walinta ko Shehinta ƙarya ce, sai tasa ita kaɗai, ita ce gaske.

11) A ƙarshen ƙarshe, Sufiy muridi, ya kai ga magaryar tuƙewa ya zama Allah (Wahdatul Wajud), domin Walinsa da Shehunsa duk Alloli ne. Waiyazubillahi. Daga lokacin komai na zunubi, ya halasta a gare shi. Idan yayi wani aikin Ibada kamar Sallah da Azumi, to na ganin ido ne, amma a zuci ba don Allah yayi ba, sai don gudun kada ragowar Musulmai na gari su zarge shi, kuma dai domin ya zama Allah a yanzu. Allah zai bautawa Allah ne? Wannan shi ake kira Zindikanci orijinal kuma lamba wan.

Annabin Rahama bai taɓa koyar da wannan ba har ya bar Duniya. Hasali ma abinda yafi so shine a kiraye shi 'Bawa Manzo'. Haka Sahabbansa da Matansa, ba su taɓa sanin wannan Ruɗanin ba, na Bawa ya zama Allah, Allah kuma ya zama Bawa. Can da ƙazantar Mushrikai.

Kaɗan daga cikin irin maganganun Shehunnansu:

Abū al-‘Abbās Ahmad ibn Muhammad at-Tijāniyy ko Ahmed Tijani:

"Albarkatun da suke kwararowa daga Manzon Allah SAW (mu fahimta anan, ba daga Allah ba) waɗanda suke kamanceceniya da Annabawa ne kawai ke karɓar su. Duk kuma abinda ya gudana ya bijiro cikin kamanceceniya ta Annabawa to kama ta ce take karɓarsa (watau yanzu ya zama Annabi a fakaice). Kuma daga gareni ne ake rabawa ga dukkan halittu tun daga farkon

Duniya har zuwa busar ƙahon (Tashin Ƙiyama) (anan kuma ya zama Allah kenan). Babu wani Wali da zai sha ruwa ko ya shayar da wani mutum ruwa, face daga Tafkinmu tun daga farkon Duniya har zuwa busar ƙaho. Ran Annabi da rai na kamar haka suke, sai yayi nuni da yatsunsa biyu, na tsakiya da manuniya. Ran Annabi yana taimakon Annabawa da Manzannin, rai na yana taimakon duk wanda yake gabas da yamma da masu haƙuri da Waliyyai tun kamin fara halitta har zuwa abada, (Minal azal ila ‘abad). Waɗannan digadigai (ƙafofi) biyu nawa, su na kan wuyan duk wani Wali tun daga lokacin Adam har zuwa busar ƙaho. Matsayinmu a gurin Allah ranar Kiyama babu wanda zai kai gareshi cikin dukkan Waliyai, kai babu ma wanda ya isa ya kusance shi, komai girmansa kuma komai ƙanƙantarsa. Kai dukkan Waliyai tun daga farkon halitta har zuwa busar ƙaho babu wanda zai kai ga matsayina". In ji Ahmad Tijjani mai Ɗariƙar Tijjaniyya.

Kunga can baya yana cewa “mu” domin fakewa da Annabi, amma a ƙarshe sai yace “matsayina”. Kenan har Annabin bai kai matsayinsa ba.

Wannan shine babban girman kai na ƙarshe da wulaƙanta ragowar Waliyan Allah salihan bayi. Duk duniya babu wani Wali wanda Walittakarsa takai Walittakar Annabawa da Manzanni da Shuhada'a da Siddiƙai da Salihan bayi.

Anan sai mu tambayi kammu, shin waye yayi masa wahayin wannan Magana? Ko molon ka ne kawai? Lallai wannan ba zai wuce kitaburra’asi ba!

Ibrahim Inyasee (Inyass):

A shekara ta 1929, lokacin da Inyass yake cikin gona a garin Kosi Mbiteyin, sai kawai ya yi da'awar **an bashi mukullin asarar ɗin Ilimin Ubangiji** saboda haka yanzu shine babban Khalifan Sufiy Sheikh Ahmadu Tijjani mai ɗariƙar Tijjaniyya, wanda wannan matsayin babu wanda ya kai gareshi a daidai wannan lokacin. A lokacin ne Sheikh Ibrahim ya kafa dokar cewar duk wanda yake son ya kai ga mataki na ma'arifa (sanin ilimin Haƙiƙa) a cikin ɗariƙar Tijjaniyya, sai ya bi ta hannunsa.

Dukka wadannan Shehunnan da ragowar irinsu, sun yarda da abinda ke littafin Jawahirul Ma’ani na Sheikh Tijjani wanda ya rubuta cewar:

- Idan ka gane shi, ka ga Annabi kuma ka ga Allah.

- Annabi ne ya bashi salatul fatih ƙiri da muzu, bayan sama da shekaru dubu da rasuwar Manzon Allah SAW.

- Ladan karanta salatul fatih ɗaya daidai yake da ladan karanta Alƙur'ani daga Baƙara zuwa Naasi sau dubu shida.

Da sauran ƙarerayi waɗanda basu sami wani goyon bayan Alƙur'ani ko Hadisi ba.

{ إِنَّمَا يَفۡتَرِى ٱلۡكَذِبَ ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ بِـَٔايَـٰتِ ٱللَّهِۖ وَأُوْلَـٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡكَـٰذِبُونَ }

Abin sani kawai waɗanda bã su yin ĩmãni da ãyõyin Allah, sũ ne suke ƙirƙira ƙarya. Kuma waɗannan sũ ne maƙaryata. [Surah An-Naḥl: 105

13 - KAMMALAWA TA GABAƊAYA.

Daga dukkan abinda ya gabata, kamanceceniyar da take tsakanin Yahudanci da Musulunci tafi yawa akan Kiristanci. Tun daga kan yiwa namiji kaciya har zuwa mafi ƙololuwar Ibada ta Tauhidi. Shi kuwa Kiristan asali ba ruwansa da yin kaciya. Domin asalin Yahudanci Tauhidi ne tsantsa kamar yadda muka gani cikin "Ten Commandments". Amma kaga Kiristanci, ya saƃawa waɗancan Addinan biyu domin abkawarsa cikin Shirka na jinginawa Allah ɗa da kuma bautawa Annabi Isa ɗan Maryam a matsayin shima Allah ne.

Dalilin jirkitar Kiristanci shine cakuɗa shi da aka yi da Maguzanci ƙasar Girka "Greek". A ƙasar Turai, tun shekaru aru-aru, kowanne abu yana da Allansa. Sai

suka wayi gari tare da shigar da wannan aƙida cikin Kiristanci, na cewa Allah uku ne.

Ya kamata a yanzu Yahudawa da Kiristoci su fahimci cewar Addinin Musuluncin da Musulmai suke bi, yana goyon bayan Addininsu na asali (wanda ba a jirkita ba), kuma dai Musulunci shi yafi dacewa da dukkanninsu, su komo su bi. Idan basu yi ba, to akalla kowa ya mutunta kowa cikin Addininsa da na ɗaya bangaren. Addininku yana gareku, Addininmu yana garemu, a zauna lafiya.

بسم الله الرحمان الرحيم

قُلۡ يَٰٓأَيُّهَا ٱلۡكَٰفِرُونَ
لَآ أَعۡبُدُ مَا تَعۡبُدُونَ
وَلَآ أَنتُمۡ عَٰبِدُونَ مَآ أَعۡبُدُ
وَلَآ أَنَا۠ عَابِدٞ مَّا عَبَدتُّمۡ
وَلَآ أَنتُمۡ عَٰبِدُونَ مَآ أَعۡبُدُ
لَكُمۡ دِينُكُمۡ وَلِيَ دِينِ

Ka ce: "Ya kũ kãfirai!"
"Bã zan bautã wa abin da kuke bautã wa ba."
"Kuma kũ, ba ku zama masu bauta wa abin da nake bautã wa ba."
"Kuma nĩ ban zama mai bautã wa abin da kuka bautã wa ba."
"Kuma kũ, ba ku zama mãsu bautã wa abin da nake bautã wa ba."
"Addininku na garẽ ku, kuma addinina yanã gare ni."
[Surah Al-Kāfirūn: 1-6]

ٱللَّهُ نَزَّلَ أَحۡسَنَ ٱلۡحَدِيثِ كِتَٰبٗا مُّتَشَٰبِهٗا مَّثَانِيَ تَقۡشَعِرُّ مِنۡهُ جُلُودُ ٱلَّذِينَ يَخۡشَوۡنَ رَبَّهُمۡ ثُمَّ تَلِينُ جُلُودُهُمۡ
وَقُلُوبُهُمۡ إِلَىٰ ذِكۡرِ ٱللَّهِۚ ذَٰلِكَ هُدَى ٱللَّهِ يَهۡدِي بِهِۦ مَن يَشَآءُۚ وَمَن يُضۡلِلِ ٱللَّهُ فَمَا لَهُۥ مِنۡ هَادٖ

Allah Ya sassaukar da mafi kyawun lãbãri, Littãfi mai kama da jũna, wanda ake ta karãtunsa, fãtun waɗanda ke tsõron Ubangijinsu, sunã tãkura sabõda Shi, sa'an nan fãtunsu da zukãtansu su yi laushi zuwa ga ambaton Allah. Waccan ita ce shiryarwar Allah, Yanã shiryar da wanda Ya so game da ita. Kuma wanda Allah Ya ɓatar, to, bã shi da wani mai shiryarwa. [Surah Az-Zumar: 23]

مَن يَهۡدِ ٱللَّهُ فَهُوَ ٱلۡمُهۡتَدِۖ وَمَن يُضۡلِلۡ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ

Wanda Allah Ya shiryar, to, shĩ ne Mai shiryuwa, kuma wanda Ya ƀatar, to, waɗannan sũ ne mãsu hasãra. [Surah Al-Aʿrāf: 178]

وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ سَنُدۡخِلُهُمۡ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَآ أَبَدٗاۖ وَعۡدَ ٱللَّهِ حَقّٗاۚ وَمَنۡ أَصۡدَقُ مِنَ ٱللَّهِ قِيلٗا

Kuma waɗanda suka yi ĩmãni, kuma suka aikata ayyukan ƙwarai, zã mu shigar da su gidãjen Aljanna (waɗanda) ƙõramu sunã gudãna a ƙarƙashinsu, sunã mãsu dawwama a cikinsu har abada bisa ga wa'adin Allah tabbatacce. Wãne ne mafi gaskiya daga Allah ga magana? [Surah An-Nisāʾ: 122], (babu har abada).

A yau:

وَمَن يَبۡتَغِ غَيۡرَ ٱلۡإِسۡلَٰمِ دِينٗا فَلَن يُقۡبَلَ مِنۡهُ وَهُوَ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ مِنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ

Kuma wanda ya nẽmi wanin Musulunci ya zama addini, to, bã zã a karƀa daga gare shi ba. Kuma shi a Lãhira yana daga cikin mãsu hasãra. [Surah Āli-ʿImrān: 85]

TAMMAT

Dukkan Yabo da Godiya su ƙara tabbata ga Allah Ubangijin kowa da komai. Ya Allah, Mai Rahama Mai jin ƙai, Ka ƙara daɗin Tsira da Aminci ga BawanKa kuma ManzonKa Annabin Rahama, Annabi Muhammad SAW, da Iyalan gidansa Tsarkaka da Sahabbansa Adalai da ragowar ManzanninKa da suka gabaceshi da sauran Salihan bayinKa waɗanda ke kan TafarkinKa Madaidaici, Tafarkin waɗanda Ka yi Ni'ima a garesu, ba tafarkin waɗanda Ka yi fushi da su ba, kuma ba tafarkin ƀatattu ba.

Bldr. Ibrahim Muhammad Ɗanƙyauri (MNIOB)
Jumada Thani 2 / 1447 AH _____ Nuwanba 22 / 2025 CE.